Dafata salma tayi tace kinkasa ganin mu ne saurin mayar da mask din Amriya tayi tace. Eh... Kubani.. Dutsen..

jan hannunta sukayi suka kaita daki
Ganin zeharis bata nan yasa tace ina.. Zeharis.  Dasu ...Aisha. nadirah tace su Aisha sun koma gida Italian yar uwarki menene mah sunanta sunfitah da Mom zata raka mom siyayya.

Meee Amriya tafada. Kalisat tace meyafaru da matsala ne. Amriya tace Aa ba matsala.

Tace Yauwa... salma..dakin.. Wana.. Shiga.. Dazu..

Dariya su nadirah suka fashe dashi fateema tace yanzu ace dukk zaman dakikayi a gidan nan bakisan wannabe dakin na waye bah toh na mom nee dakin. Tana kaiwanan nadirah tajasu suka fuce suka bar itah kadai a dakin

Rass gaban Amriya yafadi. Tareda fadin dakin mom meyake faruwa. Zaro ido tayi tace kenen hakan yana Nufi mom itace uwar shedanu dake son ganin bayan wannan ahalin.

Kenen Itace tazoda Zeharis gidanan.  Tabbas kenen itace Uwar shedanu.

Daga sama taji ance kwarai kuwa nice

COMMENT & SHARE PLS □□□□
ALKALAMIN □□□?
BABY ISHA □□□□□□
2/28/24, 22:07 - AISHA M.B (Baby isha): https://www.facebook.com/61556643936657/posts/122103978398221464/?substory_index=1596987511055341&mibextid=rS40aB7S9Ucbxw6v

JAJIRTATTU WRITER'S ASSOCAIATION □□□?
(J.A.W)
Rubutu baiwa ce daga Allah, jajirtattu ne kawai kan iya amfani da wannan kasaitacciyar baiwa su sauya tunanin al'umma cikin sauk'i □□□

ALJANAR RUWA CE □□□□□□□□□□? PAGE 2 □□□ 6 □□□□□□ 2 □□□ 7 □□□

WRITTEN & DIRECTED □□□
BY BABY ISHA □□□□
(AISHA M.B)

---

Da kaolin mamaki amriya kebinta dashi tareda fadin mom kece. Mom batajira cewarta bah tace kwarai da gsk kinyi mamakine.

Tabbas nice. Zeharis ce tashigo murmushi dauke a fuskanta tace hmm yar uwata Aljanar ruwa hatare itada Mom suka kwashe da dariya

Cikeda bakinciki Amriya tace Amma indai kece mahaifiyan Kalb baiyi dacen uwaba.

Mom tace laaa Ashe mah kin iya mgn daidai.

Toh barakiji ni na haifesa kuma saina gabadayansa.

Cikin kunan rai Amriya tace karya kike baki isah kigabayansa bah Baku isaba indai har ina gidanan kuma Koh bana nan Allah saiya tona asirinki.

Azafafe mom tace saidai Allah yatona Asirinki aljanar ruwa . Kin manta duk wanda yabi hanyar da uwar shedanu tabi sunansa gawa. Saina gabayan wannan ahalin sainasa anyi ruwan jini..

Dakata nan Amriya tafada kinsandai ni Aljanar ruwace kekuma BIL Adama babu inda Aljanar ruwa da bil adama zasu hadu Dan haka Kisani kinyi kuskure fadamin gsk kece uwar shedanu sbd bazan bar mutum daya daga cikin ku shedanuba. Hmmm yanzu wasan yasoma.

Matso daff da Amriya mom tayi tareda fadin muzuba mugani. ALJANAR RUWA KOH KUMA UWAR SHEDANU

Juyawa su biyun sukayi daniyan futa dakatar dasu Amriya tayi dafadin kada ku manta ku hada makamanku Dan nawa makaman ashiryesuke.

Murmushi mom Da zeharis sukayi tareda fucewa daga dakin.

Dafe kanta Amriya tayi wasu zafafan hawayee nabin kuncinta tace Meyasa sai ke Mom meyasa zaizamana kece Maison ganin bayan wannan ahalin tabbas bazan barki bah dole nadaka tardasu yazama dole nasanar da Aunty Amarya.

Direct part din Aunty Amarya tanufah. Ta tarar da triplet acikin dakin .

Adeef yace yauwa Aunty gatanan mah tashigo kimata mgn Dan Allah.

Kiran Amriya Aunty Amarya tayi kusada itah. Zuwa Amriya tayi kusada anty Amarya tace gani aunty.

Aunty Amarya tace kinaji yan uwanki guda biyu waike suke so . Rass gaban Amriya yabada. Tace Nikuma Aunty meyasa saini.

Adeef yace kada Kice haka inason zan aureki ne kawai indan bakyaso toh saina hakura.

Amar yace amma wannan bayi bane naga dai naruga ka. Shikenen Amriya tace tareda fadin Aunty duk Abunda kikace shine daidai.

Aunty Amarya tace Aa amriya bafa iyasu bane khaleed mah yazo yafadamin yanzunan yasanar dani.

Hatare su Mom, grandma, dad, khaleed da sadiq dasu nadirah sukashigo tareda fadin kwarai kiss yar mu.

Dad yace yakamata muma ace yaran mu su samu Mace tagari irinki Amriya. Dafata mom tayi saurin cire kafadarta Amriya tayi tareda watsamata banzan kallo cikin murmushin yake Mom tace yar mu yakamata kizabi daya daga cikinsu koh.

Tunda Sun sanar dake abunda ke cikin zuciyansu.  Murmushi Amriya tayi tareda fadin ehh zanyi tunani akai. Cikin ranta kuwa tace waiyoo Allah meke damun ahalinan rayukansu nacikin hadari sukuma suna min mgn aure. Taya Aljanar ruwa zata auri BIL adama abunda bazai taba yiwuwa bah kenen

Dad yace toh yata Allah yasa muji Alkhairy

Nadirah tace Amma bakaramin dadi zamuji bah idan kika zamo matar daya daga cikin Dan uwanmu.

Fucewa gabadayasu sukayi . Ajiyan zuciya Amriya tasauke. Tareda rikee hannun aunty Amarya tace Inason zanfadamiki wani abu.

Aunty Amarya tace menene fadamin.  Amriya tace bah lallai kiyarda Dani bah idan nafadamiki Amma kisani tanaso taga bayan Ahalinan.  Aunty Amarya tace ban fahimta bah Amriya wacece zatagabayan ahalinan.

Uwar shedanu mana. Amriya tafada. Tareda fadin wai Mom itace uwar shedanu .Aunty Amarya tace Mom. Kwarai Amriya tafada.

Murmushi Aunty Amarya tayi tareda fadin Nasani. Amriya tace kinsani kuma baki taba fadamin bah.

Aunty Amarya tace nafison kigano da kanki kuma yanzu kingano.

Amriya tace indai kuwa hakane bazan bartabah har ita zeharis din. Meeee zeharis kuma meye hadin zeharis yar uwarki kuma.

Bakomai Amriya tabata amsa.

(AFTER ONE WEEK)
kowa nagani a parlour a zazzaune. Kowa da abunda yake sakawa a ransa.

Dad yace muna jiran cewarki Amriya. Wa nee kikaga yadace da rayuwanki sai mubaki shi kizaba nikuma namiki alkawarin zan Aura mikishi.

Kallon Aunty Amarya Amriya tayi. Fatan nasara Aunty Amarya tayi mata.

Kallon kowannensu Amriya tayi tace ina mai gdy agareku ... da kuka ...bani.... wannan.. babban... daman ....a ..gsk ...yau... zanfadi wanda ....ke ...raina ...zan ....aura. ...A gsk..

Grandma tace toh ennen kifada mana saikin jamana rai kuma. Daidai lckn dakuma kabir kesaukowa daga upstairs.

Amriya tace a gsk.... Ni... Kalb... Nakeson... Zan... Aura...

Kabir Jin maganan yayi uwa aradu da kallon mamaki kowannensu kebinta dashi .

Dad yace shikenen yata aure ki kaddara andaura angama wanna Kalman dama  nake jira kenen saikuma Allah yayi Kinfada. Sosai kowannensu yayi Murna furucinta. Dad

yace khaleed zanbaka Fateema, kaikuma sadiq nabaka yata nadirah triplet Abdul yace nidama inada kalisat dita. Amar yace inason ummi.  Adeef mah yace abani Aisha Dad.

Toh Alhamdulillah Insha Allah next month za'ayi baikon maza uku khaleed, kabir dakuma sadiq daga baya kuma anyi naku. Dama munruga damun yanke wannan shawarar da mamin ku dakuma uncle dinku Dan haka idan akwai mai jaa a mgn tah yafuto yafada

Daga sama sukaji nadirah tace bazai yuwuba wlh bazan yarda bah tana kaiwanan ta nufi hanyar daki da gudu. Su salma suka rufa mata baya.

Kabir yace Dad Dan Allah Dad kada ka Auramin itah wlh banason tah bana kaunarta idan na aureta bazan tabayin farinciki bah.

Grandma tace kaiii menene haka Kanaso kana kaiwa kasuwa. Toh dole sai anyi auren koh kanaso koh bakaso.

Sosai su khaleed basuji dadi bah ha hankali kowanensu yabar palourn.
Dad yace Amriya insha Allah cikin kwanan nan keda mijin ki na gobe zakutafi Dubai siyayya kayan dakinki.

Kabir kamm jiyayi uwa ya kwallah ihuuu tsabar takaici da bakinciki.

Fucewa Amriya tayi daga palourn ta nufi parlour aunty Amarya.

Tarar da Aunty Amarya tayi kan kujera Da sauri Amriya tanufah inda take tace Aunty Amarya meyasa zakice nace Kalb nakeso. Bayan itama nadura nasonsa dawane ido kike tunani zasudunga kallona dashi nida nazo karban zobena nakoma idan fah nayi aurenan ban koma bah da zoben mutuwa zanyi. Indan lckn da haka irgamun yayi.

Cikin rashin fahimta Aunt Amarya tace bangane bah mekike nufi wane zobe kuma.
Dafa kanta Amriya tayi tadago da brown eyes dinta wanda suka kara rinewa sosai tace.

Aunty Amarya a gsk niba mutum bace kamar yadda kikayi tsammani ni ALJANAR RUWA CE.  Mikewa Tsaye Aunty Amarya tayii tareda fadin ke Aljanar ruwa ce.

Kwarai da gsk Amriya tafada tareda fadin nazo duniyakune kawai Dan Nakarbi zobena Nakoma. Bawai nazone Dan na cutarda kuba.

Kuma yanzu kwanakin da haka gindayamin nada komawa teku Dada jaa yake Dan Allah kidakatar da auranan banzo gidanan dan nakarbi farinciki wasubah .

Aunty Amarya tace idan ke bah mutum bace taya toh yazamtoh kikeyin period.

Amriya tace nima bansani bah,  aunty Amarya tace kenen hakan yana nufin kinada Halaka da jinsin mutane kenen.

Amriya tace jinsin mutane kuma taya ni ALJANAR RUWA CE kuma banda kowa Banida yan uwa sai Aljanun ruwan damuke rayuwa tare harzuwa girmana .  Taya zakice inada halaka da jinsin mutane.

Kwarai kuwa Amriya mgn tah ba karyabane tabbas.  Kedin ruwa biyu ce Ba iya Aljanar ruwabah tabbas kinada hadin Jinin da mutane.

Dan Allah aunty Amarya kidaina fada kibarni naji da abunda kedamuna. Gashi mom tanason Ganin bayan wannan ahalin gashi zan auri Dan tah dawane ido kenen su nadirah zasu dunga kallona dashi.

Aunty Amarya tace su kalle kidin mana sundade basuyibah kenen sokike rayuwansa ta salwanta a hannun wannan shedaniyan matan idan baki aureshibah taya zaki iya dakatar da mugun abu dazai tinkaroshi.

Bayan kuma indan yaje ya auri wata matan Matar bazata bari kidunga zuwa kusada shi bah.

Amriya tace Meye Anfani kyautata wah wanda baison kanamasa hallaci bah  ya tsaneni koh da yaushe
bashida wata mgn daya wuce na tsaneki banason ganin ki.

Hantara,  zagi,  Shaka,  Duka, wanne bansha bah awajansa tun kafun na aureshi kenen idan na aureshi mah abunda zaiyi saiyafi haka  bazai yuwubah takasheshi din itah ta haifi abunta. Amma wannan ahalin bazan Bari ta cutardasu bah koda kuwa Hakan shi zaizamo sanadiyan daina numfashina.

Aunty Amarya tace Amriya kawo kunnenki kiji  datsa kunnenta Amriya tayi a saitin bakin Aunty Amarya.  Saida Aunty Amarya tadau kusan 2minutes tana fadamata mgn.

Amriya tace Amma kin tabbata hakan zai yuwu. Anty Amarya tace kwarai da gsk

Shikenen baranje. Futa amriya tayi daga dakin tanufi dakinsu saida tadan tsaya. Tukunan tashiga.

Suna ganinta suka mike tsaye.  Nadirah fuskanta shabe shabe da hawaye tace mayaudariya macucuciya na tsaneki wlh. Banason ganin ki kifutamana daga gida.

Amriya tace. Dan.. Allah.. Ku.. Fahimceni. Tasss tass Nadirah ta tsinka mata maruka har guda biyu.  Dafe kuncinta Amriya tayi hawaye sukafarabin kuncinta.

Daff da Amriya salma taje tareda tofa mata yawu a fuska tace Allah wadaranki maciya amana
Sosai Zuciyan Amriya ke bugawa tsabar damuwa.

Kalisat tace kin bamu mamaki Amriya a fuska uwata Allah Amma azuciya ke shedaniyace. Macuciya. Kawai. Bamuason kara ganin ki munafuka Kawai

Tsugunawa Amriya tayi kan gwiwowinta tareda hada hannuwanta tace Dan Allah.. Ku.. Fahimceni... Ku.. Saurareni.. Kunyimin.. Mumunan.... Nadirah bata bari takarasa bah ta dauki glass cup tareda rotsawa kan Amriya. Faduwa Amriya tayi jini yafarabin kanta.

Nadirah tace ke macuciya duk irin soyayya da na nunamiki duk irin soda kaunan danake miki bantaba banbantaki da sauran yan uwana bah kayanda nakesa shikikesawa Komai nawa nakine Amma yau kika butulce mana. Kinci Amana yan uwantaka damuka nunamiki.

Dan Haka dole kifuce mana daga gida yanzu Dan idan nacigaba da kallonki zan iya kasheki .

Fateema tace bakiji abunda tace bane maza kifuce.  A hankali Amriya ta mikee hannunta dafe da goshinta wanda ke zubar Dajini.

Murmushi su Mom dake labe sukayi mom tace hmmm bakiga komai bah ALJANAR RUWA wannan wahalan yanzu kikasoma shansa wlh  wannan sammo tabine. Tunda kika sa Gabadaya shirina ya ruguje kema saina sa Duniya ta gundureki.

ZeHari's tace dole idan munason mukara karfi kizamo uwar shedanu na gabadaya duniya sai mun karbi zoben Hannu kabir sannan zakizamo uwar shedanu nagabadaya duniya babu wataa koh wani dazai iya jaa dake.

Mom tace kwarai kuwa wannan duniyan ta ninikadaice. Barin kofan dakin sukayi.

Damkar gashin kan Amriya nadirah tayi tareda zubamata wani marin haka sukashiga marinta ba kakkautawa.  Saida jikin Amriya yayi tsami bah Abunda takeyi sai rokon su

Daga karshe salma tazage ta naushi cikinta wani irin azababban kara Amriya tayi.

Faduwa Amriya tayi tafara numfashi sama sama hawaye nabin kuncinta. Tari Amriya tafarayi. Da alama asmanta ne yatashi.  Kallon inhelar dinta tayi kan table. Jan jikin tah tayi tango inda inhelar yake.

Ture table din salma tayi inhelarn yafadi kasa. . Ummi kamm inbanda kuka bah abunda take.  Hakuri ummi tashiga basu amma koh kallo bata ishesu bah..

Sosai numfashin Amriya kesama sama. Nufan inda inheler yafadi tayi tareda mika hannunta zata dauka taka Hannun nadirah tayi. Ritsee idanuwanta Amriya tayi hawaye suna zarya a idanunta.

Sosai zuciyanta ke bugawa da karfi karfi. Ganin zasu iya hallakata yasa ummi futa waje da gudu.  Bataga kowa a parlour bah hakan yasa tango dakin su kabir.

Tarar dasu tayi kowanne yana aiki a system. Dago kai Khaleed yayi tareda fadin kee lfyn ki zakishi go mana daki bah sallama.

Cikin rawar murya ummi tace tanachan..zasu.. Kasheta. Khaleed yace wah za'a kashe ummi tace zasu kashe Amriya gashinan sunata dukanta Dan Allah kaje Ka dakatardasu.

Da sauri khaleed ya tashi suka nufi dakin.  Nadirah tace Kalisat daukomin wuka. Direct kitchen kalisat tanufah ta dauko wuka Mika wa nadirah wukan tayi.  Daga wukan Nadirah tayi tace badai sbd kinaji da wannan kyau naki da gashi bah toh yau zan bata fuskan nakuma yanka gashin daga wukan Nadirah tayi zata yanka fuskan Amriya.

Rikee wukan fateema tayi tareda fadin Nadirah yakamata mubarta haka basai kin lalata mata fuska bah. Mu kyaleta hakan mah taji ajikinta.

Fusge hannunta nadirah tayi tace wlh bazan baribah tasan shekarunawa nayi inadakon sonsa saikuma itah banza Chan zata ruguzamin soyayya tah bazaiyubah.

Daidai fuskanta takai wukan Domin tsaga fuskan.

Sukaji am bankoh kofan itakoh Amriya tuni ta Suma tsabar jigatan datayi.

Kallonsu khaleed yayi da rinanun idanuwansa
Tareda maida kallonsa kan Amriya zaro ido yayi ganni yadda goshinta yayi jina jina da jini ga fuskanta shatin maruka

Daukanta khaleed yayi yanufi hanyar waje da itah.

Sharaff suka hada ido da kabir wanda ya harde hannuwansa guri daya.
Kabir take waya baka izini daukan wacce zan aura. Khaleed yace kabir yanzu bah lckn wasa bane yakamata mukaitaa Asibiti zata iya mutuwa su nadirah ne sukayi mata haka.

Kabir yace toh ka ajeta ta mutu mana saime waya damu. Khaleed yace kasani kabir koh kanaso koh bakaso ita zaka Aura kuma da itah zaka Karachi rayuwanka kasani cows idan kacigaba da wannan halin naka sai an wayi gari a lckn da kake bukatarka a lckn zaka rasata.

Da sauri yabar wajan tareda nufah cikin mota ya aje tah sannan yaja motan yabar gidan direct asibity yanufah da itah . Tareda Korans Mom da Dad. Awaya yasanar dasu halinda amriya keciki.

Bangaran kabir kuwa ranshi yakai kololuwar baccy gamida abunda sukayiwa Amriya yazare bellit dinshi yayi yanufi dakisu nadirah.

A firgice su nadirah suka mike. Sukafaraja da baya kabir yace ku kwantar da hankalinku bawai kasheku zanyi bah duka ce kawai zakusha.

Baiyi wata wata bah yafara dukansu tako ina saida yadau wajan 30 minutes yana jibagansu saida yaga sunyi laushi sannan yabarsu yafuce daga dakin

Chakk kabir ya tsaya jin hana kuka acikin daki.
Direct dakin yanufah tareda shiga ciki. Dawani irin karfi kofan ya rufe kansa.

Kura da datti ne kawai kake gani a dakin.

Zaro ido yayi gani wata mata jikinta buzu buzu gashin kanta Yabaze uwa mahaukaciya.
Jikinta daddaure da kaca . Kallonshi tayi tace zata kasheka waccan matan azzaluma ce .

Kabir yace wacece kee mekike hanan wajan.
Ni nice bazato ba tsammani yaji an bugamai karfe akai faduwa yayi sumamme.

A fusace matar dake daure tace mene haka meya miki Muguwa azzaluma tabbas bazakiyi kyakyawan karshe bah

Dariya Mom ta kwashe dashi tace bayau hakafara fadamin wannan bah Dan haka kisa a ranki wannan gidan yakusan zamo makabarta.

mika hannunta Zeharis tayi domin cire zoben hannun kabir jitayi anyi sama da itah sannan haka nakata da kasa.

Faduwa tayi bakinta yafara binda jini.  Murmushi Matan tayi tareda fadin kuna tunanin zaku iya taba ku zauna lfy.

Kuna tunanin zaku iya taba mijin Aljanar ruwa kuma kuci bulus.  Hmmm tabbas akwai kallo gaba,  kinsa mutane da dama kunci rayuwa,  kin kashe mutane wanda bazasu irgu bah Dan kawai sbd abun duniya  . Kisani ALJANAR RUWA saita gah karshenku.

Ina kike nee Aljanar ruwa kifuto ki dakatar da muguwan matan nan daga zaluncintah

. firgit amriya ta farfado daga baccin datake kallon ko inatayi taga ai a asibity take rintse idanuwanta tayi tareda bacewa daga hospital din.

---
TOH FAN'S MENENE RA'AYINKU GAMEDA WANNAN MATAN SHIN WACECE ITAH MENE LAIFINTA DA MOM TA DAURETA

MEJEDAI ZUWA AKWAI KALLO GABA FAH.

COMENT PLEASE
ALKALAMIN YAFI TAKOBI □□□□

WRITTEN BY BABY ISHA □□□□
2/28/24, 22:07 - AISHA M.B (Baby isha): https://www.facebook.com/61556643936657/posts/122103978398221464/?substory_index=1596987511055341&mibextid=rS40aB7S9Ucbxw6v

JAJIRTATTU WRITER'S ASSOCAIATION □□□?
(J.A.W)
Rubutu baiwa ce daga Allah, jajirtattu ne kawai kan iya amfani da wannan kasaitacciyar baiwa su sauya tunanin al'umma cikin sauk'i □□□

ALJANAR RUWA CE □□□□□□□□□□? PAGE 2 □□□ 8 □□□□□□ 2 □□□ 9 □□□

WRITTEN BY AISHA M.B (BABY ISHA) □□□□.

---
Kara rintse idanuwanta tayi amma saitaga still bata bace ba dafa ta taji anyi. Da sauri amriya tadago idanuwanta tadora hakan nata. Murmushi doct Amina tayi tareda fadin yajikin naki yata.
Da sauki Amriya tafada muryanta a dashe tsabar tasha wahala.

Yusuf ne yashigo hannunsa dauke da magunguna.  Ya mutse fuska doct Amina tayi tareda fadin Kai tundazu dana aikeka balsam zaka dawobah sai yanzu

Yusuf yace haba my one  Dan Allah kiyi hakuri wlh wannan surukarkice tadameni. Hartasa namanta da aikena kikayi amma hayimin afuwa Dan Allah kinji.
Nakidin cewar doct amina zama yusuf yayi yashiga bata hakuri. Tareda jaa mata kumatu. Sosai Suka burge Amriya.
Karban maganin doct Amina tayi ta ballawa Amriya shigowa Khaleed dasu Aunty Amarya sukayi.  Kallon Amriya sukayi sukaga ta rame sosai. Daff da itah Aunty Amarya taje tareda fadin yata yajikinki. Amriya tace da sauki. .....

Murmushi mom tayi tace idan bazai dauku bah idan na taka zan dauka kuma wannan zoben raunin Amriya yake Dan haka saina azabtar da itah saitin hannun kabir mom tasa kafarta.
Matan dake daure tace Aa karima kada kiyi haka na rokeki kibarshi. Zaki iya haddasa wani abun.
Ko kulata mom batayibah tadaga kafanta daya tareda taka hannun da zoben kesanye ajiki da mugun karfi

Wani azababban kara Amriya tasaki. Sosai hankalinsu Doct Amina danasu khaleed yatashi. Tambayanta sukafarayi meyasa Meta.
Tashi tsaye Amriya tayi hatake wani irin jiri yadauketa tafadi. Rintse idonta tayi tace Mom, Mom, mom, bazan barki bah, tabbas kinfara wuce iyakarki.

Dafata Aunty Amarya tayi tareda fadin menene yafaru Amriya. Kallon Aunty Amarya amriya tayi tareda fadin yakamata... Mu.. Tafi.. Gida. Yanzu..

Aunty Amarya tace gida kuma bayan bakigama samun lfy bah..

Amriya tace inason muje gida yanzunan ba bata lck.  Ganidai da gsk Amriya take yasa Aunty Amarya daukan Jakarta ta faraway Amriya jikinta. Tareda rikee Gambits zasufuta. Doct Amina tace ina kuma zaki yadda itah bayan bata gama samun sauki bah.

Aunty Amarya tace zamu tafine sbd akwai muhimiyar aiki dazamuyi. Yusuf yace aiki kuma dama mara lfy yana aikine.

Kallonsu Aunty Amarya tayi tareda fadin Bazaku fahimta bah.

Fucewa sukayi daga asibityn da kallon mamaki khaleed yabisu dashi.

Direct cikin gidan sukashiga basutadda kowa a parlour bah.  Idanuwan Amriya ne yasauka hakan na Kabir wanda ke kwance hakan liners gefe kuma Mom dasu grandma ne azauna. Ba abunda mom keyi sai hawaye  .

Da sauri Amriya ta isah garesu. Rikee hannunsa tayi taga yayi jajir. Ga zoben a hannunshi yasauya Kala.

Azafafe Amriya ta juyo ta maida kallonta kan Mom.  Murmushi Mom tasakar mata.

Zare zoben Amriya tayi tasaka a hannunta. Kallon Zeharis taxi tace yar uwa Dan Allah kizo kitayi daukan abu a daki. Amriya nagama fadin haka tashige daki.

Babu jinkirtawa Zeharis tabita. Ciki.

Zama Amriya tayi kan gado gambits rikee da kanta. Shoppes zeharis tayi tareda fadin gani Aljanar ruwa mekikeso nayi miki.

Azafafe Amriya ta tashi tareda shake wuyan zeharis. Tace me kukayimai ehhh kifadamin kafin na kasheki yanzu ture Amriya zeharis tayi tareda fadin kee bafa tsoronki nakeji bah.

Idan kinaso kisani toh muje filin daga mu gwabza tsakanina dake. Murmushi Amriya tayi tareda fadin shikenen muje. Rintse idanuwansu gabadaya sukayi, daga bisani suka bace daga dakin

Basu zarce ko inaba saicikin daji kallon ko ina Amriya tayi tareda fadin meyesa kika kawoni nan.

Wani irin dariyan mugunta, zeharis ta busheda shi, tace nakawokinan nee domin kiga yanda zan kashe masoyinki. Kabir.

Karya kike Kalb yana gida kuma ba abunda kuka isah yimai.

Wani dariyan zeharis takuma fashedashi tace ohh da kina tunanin wancan damuka aje shine kabir din toh wancan na bogine bashiba.

Amriya tace ina kuka kaishi kisani idan yaji koda kwarjane ne bazan barku da rankuba.

Murmushi zeharis tayi tace kalli Chan kigani mana Yar uwa.

Kallon inda zeharis tanuna mata tayi idanuwanta ne yasauka hana kabir dake cikin dutse gunki Ba alaman numfashi a tattareda shi.

Kallon Zeharis Amriya tayi tace menene hakan meyasa zakusashi acikin wannan abun.

Zeharis tace sadaukarwa mana zamu sadaukar da rayuwansa ne ga qungiyar mayuuu wacce Uwar shedanu zata zama.
Kuma rana na fadi zai sheka.

Zeharisssssssss Amriya tafada a transfer tareda nufo inda take.
Zeharis batayi wata wata bah. Tayi sauri tanufi inda kabir yake tareda danna yatsan Hannusa.

Faduwa Amriya tayi tareda rikeee saitin zuciyanta.
Tace zeharis kibari, kada kikara taba wannan zoben.
Zeharis tace da gsk Kisani toh tunda kika zubar mana daga mulki.mu nafara kudirin niyar kasheki a yau kuma burina zai cika.

Zan kasheshi sannan nazo na kasheki..  Takobi naga ta dauka ta nufi inda kabir keep kwance bah bu jira Amriya ta daka tsale tayi kan Zeharis.

Tareda dagata sama ta nights jikin bishiya. Faduwa Zeharis tayi tafara

Saukan da numfashi,  daukan takobin Amriya tayi Tareda nufah inda zeharis take bata yi Wata wata bah ta caka wa zeharis aciki.

Wani azababan kara zeharis tasauke daga bisani tayi tsit ba alaman rai tattareda itah. Tashi Amriya tayi tace saina gabadayanku bakidaya.

Mom, alhj Islam dakuma sauran yan qungiya kujira baiyyanata agareku. Saina dandana muku azaba. Bazan kashe ku bah saidai zakusha azaba.

Inda Kabir ke kwance ta nufah. Dagoshi tayi tareda rungumesa kamm ajikin tah. Wasu zafafan hawaye sukafara  bin kuncinta.

Rintse idanuwanta tayi suka bace daga wajan direct dakinshi Amriya ta kaishi tareda kwantar dashi kan gado ta lulubeshi.

Fucewa tayi daga dakin taga babu wannan kabir na bogin da haka aje.

Direct Dakinsu nadirah tashiga.  Su nadirah naganinta suka mike tsaye. Salma tace meyakawoki banza maiyya kawai.

Amriya tace kada kikara kirana da suna maiyya sbd niba maiyya bace.

Zaro ido gabadaynsu sukayi. Nadirah tace dama ashe kin iya mgn tabbas Salon yaudaranki ya burgemu. Kowa dake gidanan saiyaji wanan mgn

Amriya Tace Dan Allah kutsaya ku saurareni.

Fateeema tace baza mu tsayaba. Muguwa wato sokike keda yar uwarki maiyyan chan ku kashemana Dan uwa shiyasa kikeson ki aureshi. Macuciya kawai.

Dama farko yaya khaleed ya tsane ki. Saiyanzu mah nake nadaman daina tsananki dayayi sakamakon muna hanasa ashe dama kedin yar basaja ce. Yar leken asiri.

Amriya tace niba haka nake bah. Nadirah tace toh ya kike, murmushi Amriya tayi tareda fadin nan gaba zaku sani .

Yanzudai ba wannan bah Salma ina dutsen dakika dauke min. Salma tace bansanibah kuma yana wajena bazan bayarbah.

Zama Amriya tayi wasu hawaye na shirin zanies da sauri ta share tace Allah sarki ni. Marainiyan Allah, na tabbata da iyayena na raye bazan fuskanci wannan muzancin bah.

Shikenen zan bar Muku gida Zan tafi naje na nemo iyayena koda hakan zai yi ajalina.

Tashi tsaye Tayi da niyyar futa da sauri sukasha gabanta. Nadirah tace ina kike shirin tafiya.. Amriya tace zanje nemo ahalina nee.

Kalisat tace wane ahali bayan gamu. Nadirah tace idan kika tafi kika barmu kina zamu iya rayuwa bake. Dawani irin sauri gabadayansu suka rungumeta.

Tsugunawa gabadayansu sukayi Nadirah tace Dan Allah Amriya kiyafe mana hakan abunda muka aikata miki. Sbd soyayya ta rufemin ido nakasa gane gsk Dan Allah kiyafemana.

Murmushin jin dadi Amriya tayi tace nidama Baku mun laifibah. Kodayaushe kuna cikin tunanina meyasa zansaku a rai bayan kun mun komai.

Tashi Amriya tayi tsaye tace inason kafun na auri Kalb na baiyyana muku ni wacece.

Nadirah tace kamar ya kenen . Amriya tace kwarai kun min hallacin dabazan taba mantawa bah Dan haka yau na yanke cewa zan fadamuku asalin wacece ni duda ba lallai kukara zuwa inda nake bah.

Fateema tace mufah bamu fahimta bah. Ummi ce ta banko kofa hannunta rikee da cup da alama ruwane aciki.

Kafanta ne ya buge jikin table inaaa sai ruwan ajikin Amriya. Ba'afi 2second bah Amriya tazama Aljanar ruwa.

Wani irin kara Gabadayansu sukasaki. Daga bisani sukayi shiru da alama Sun suma. Friday lckn kuma Aunty amarya keshigowa.

Watsamusu ruwa tayi sukafarfado. dawani irin sauri suka koma bayan aunty Amarya. Nadirah tace aunty wlh zata kashemu kitaimaka mana.

Murmushi Aunty Amarya tayi tace ba 'a abunda zatayi muku asalima itadin mai taimakawa ce bamai cutarwa bahh. Zaman dasu Aunty Amarya tayi kan gado.

Sannan taje tadauko towel to gogewa Amriya bindinta ba'a fi two minutes bah Ta koma Mutum.

Fateema tace idan harke aljanar ruwace taya zaki iya auran mutum bayan kee ba jinsin yan adam bace.

Aunty Amarya tace Bawai auranshi zatayi dundundun bah tanaso ta taimakawa wannan ahalinne daga wajan shedaniyan matan chan.

Kuma ta taimaki kabir. Kabir kuma salma tafada. Toh ku
bude kunnuwanku kuji tundaga abunda yakawo amriya gidanan Amriya tafada musu. Amma bata fadamusu cewan Mom itace uwar shedanu.

Dawani irin gudu sukaje suka rungumeta. Nadirah tace ba bukatar jin storonki Amriya sbd kedin bamai curates bace kedin tadaban ce.

Inkoh hakane idan muka gano wacece lord lady bazamu barta bah tunda bayan ahalinan takeson gani. Amriya tace yanzu kundaina jin storon nawa.

Dariya suka kwashedashi Nadirah tace kozaki Dan kara nunamana bindin kii.

Amriya tace Aa bazan yidinbah. Akwan saikin yii ummi ebomana ruwa. Amriya najin haka tafuta dagudu tana dariya rufamata baya sukayi gabadaynsu dariya dauke a fuskokinsu.

1weeek later

Kabir inason kasaurareni da kyau kada kace zaka nuna halin naka achan kasar waje. Ka kula da Amriya kamar kanwanka ta jini banason naji wani abu sabanin haka yafaru.

Kabir yace insha Allah Dad zamu kulada itah. Amma dad ina da tambaya. Idan kabani daman fada. Dad yace inajinka son.

Dad a yanda nasani iyaye susuke zuwa su siyo kayan lefe da kayan daki apart from iyayema, ni kadai mah zan iya zuwa Amma meyasa saina tafida itah.

Grandma tace ohh nii halimatu sadiya wannan yaron uwa Dan Aljnanu tsabar naci a mgn. Toh barakijini nan zakujene domin kawai kukara dankon soyayya kajini koh. Kuma naga ai ba iya auranka za'a yi bah harda nasu habu dakuma kaluud. Suma ai zasuje su siyoma matayensu kayan lefe.

Murmushi Dad yayi yace zakasani son idan kundawo kawai kutafidai. Karkurasa flirt.

Inafatan dai Dubai zaku koh Kabir yace bah kasar dubai zamu jee bah kasar Ethiopia zamu.

Wasu irin hawaye ne yakeshirin saukoma Dad dasauri yashare idon tareda fadin asauka lfy.yauwa Amriya kwananan bana ganin wannan yar uwanan taki.. Amriya tace ohh... Tacemin.. Zata.. Tafi.. Gidan.. Mujinta.. Ne. OK that's good.

Yana kaiwanan ya wuce daki. Aunty Amarya naganin haka ta bi bayansa.

Daukan photon first wife dinshi yayi yafara shafa fuskanta tareda fadin nayi kewarki fatima Tabbas ban cika Alkawarin dana daukan wah iyayenki bah.

Shiga dakin Aunty Amarya tayi tareda zama kusada shi tace ka tunaninta nee Haba Dad Kabir kasan fah bakyau yiwa mamaci kuka.. Yakamata ace adua kakeyi mata sbd ruhinta yasamu salama.

Koba komai zatayi farinciki .. Nasani zainab tunda ta rasu nake tunani kasheta hakayi ba wai gurin haihuwa ta rasubah.

Haba dad kabir Menene hakan aikasan wasu suna mutuwa wajan haihuwa.  Dad kabir yace kwarai da gsk amma wata doct cee tasamun tantama harna shekara da shekaru bandainaba kuma bandaina bincike aike bah.

But what i know is that Fatima was killed by someone.. Aunty Amarya tace koh kasheta kokuma hakasin haka taruga data barmu adua mu kawai take bukata.

Ance zato zunubi koda yakasance gsk kawai Adua zaka dungayi Allah ya baiyyana gsk lamarin.
Nagode zainab hakika kedin mace tagarice inafatan kema bazaki barnibah kamar yanda fatima ta tafi. Murmushi Aunty Amarya tayii tareda fadin insha I will stay with you my husband till deat do us part.

Allah yamiki Albarka matata. Ameen Aunty Amarya tace. Dad yace that's reminds mee wai ina karima takene. Aunty Amarya tace ohhh dazu tacemin wai her sister batada lfy tace zata tafi. Wayanka baya shiga shiyasa tacemin idan Kadawo nafadamaka.

Girgiza Kai kawai yayi.

Su kabir kamm Direct airport suka nufah. Sadeeq yafuto musu da boxes dinsu guda biyu.

Amriya kamm inbanda zazzare ido ba abunda takeyi.

Kallonta kabir yayi yace keee muwuce mutafi. Amriya tacee ba.. Inda.. Zani.. Inajin.. Storo.

Wani irin kallon banza kabir ya watsa mata
Yace alhamdulillah nima dama basonake kije bah barana kira daya daga body guard su komardake gida. Kohkuma ki hau napep ki tafi.

Sadeeq yace amma fah kabir bakada mutunci kinga Amriya tawo muje.

Basu sukakai Ethiopia ba sai bayan 4hours.

Futowa mutanen cikin jirgin sukayi. Daya bayan daya.

Rikee hannun Amriya khaleed yayi. Shiko kabir yabita sakanin hannun ya wuce da kallon mamaki su khaleed suka bishi dashi.

Direct hotel suka nufah inda kabir yace Jana's daki hudu. Sadeeq yace Mezamuyi da daki harguda hudu daki biyu ya isah.

Kabirr yace toh itah wannan din a ina zakusata hakaina. Koka mee. Khaleed yace da da halin zama hakan naka data zauna amma ba hakan zata zaunaba a dakinda zaka zauna zata zauna.

Impossible kabir yafada nida wannan din zan zauna a daki daya. Wannan bazata taba faruwaba , sadeeq yace kabir why are soo arrogant.
Toh a dakin naka zata zauna kayi duk abunda kake tunanin zaka yii.

Room dinda haka bashi shida amriya yanufah tareda ajee jakansa yashiga toilet domin watsa ruwa. Tareda dauro alwala.

Itako Amriya gabadaya zaman jirgin ya sa tagaji sosai. Hakan yasata kwanciya hakan makeken gadon.

Suko su khaleed tuni sukashige dakinda haka basu.

Futowa kabir yayi yaga tayi shememe hakan gado. Sallah yayi tareda yin azkhar. Yatashi kallonta yayi yace she's not Bad. Tanada kyau, lck daya kuma ya ya mutse fuska.

Tareda Jan gashinta da karfi azabure Amriya ta tashi. Kee bakasheki zanyi ba kitashi kije kiyi Alwalah kiyi sallah. Amriya tace nayi ..sallah.

Kabir yace agidan ubanwa kikayi toh idan sanda kike harkan barikinki nee toh kiyi dubunai shekaruma karkiyi Amma kinatareda kabir nee yin sallah wajibine. Before i show you my true Colour go now.

da alama gabadaya Amriya bata fuskanci meyace bah.

Tace. Magana.. Kayine.. Cikeda takaici kabir yace Aa bah magana nayi bah waka nakeyi. Wato tsabar kin maidani mahaukaci nayi mgn kuma kina tambayata mgn nayi tashi kije kiyi sallah ko ranki ya bacii banason bujiramewa Dad dina amma datunan kisha mari wlh.

Tashi Amriya tayi tanufi toilet tadauro alwalah tayi sallahn taa. Ta tashi tanufi kan gado inda yake

Dakamata tsawa yayi kee ina kike shirin zuwa. Amriya tace kwanciya.. Zanyi..

Kabir yace ni dake a gado daya impossible, na iya hada gado daya da karuwan titi.

Amriya tace. Toh.. A ina.. Zan kwana.. Nunamata kan sofa yayi yace ga sofa Chan kije ki kwanta hakai.

Bah musu Amriya tanufi sofan tareda kwanciya hakai. Sosai A.C dakin ke ratsa jikin tah rungume jikinta tayi hakoranta sukafara karkawa.

Kashe wutan dakin Kabir yayi ai Inaa Amriya tamike zunbur. Tareda lalubo inda wutan yake ta kunna.

Tashi kabir yayi yace kee menene hakan. Ehhh.  Amriya tace bana.. Iya.. Kwanciya.. Cikin duhu.

And soo Kabir yafada ina ruwana inbakya iya kwanciya a duhun banda shashasha dalla kashe mun wuta kafun kisha hannun maza. Wlh

Bah musu Amriya takashe tanufin kan sofan tareda kwanciya.
Sosai takejin sanyi nashigarta, gabadaya sanyIn nadada shigarta. Hatake jikinta yadau zafi. Hakoranta ne suka fara karkarwa.

Kabir kamm jinta isheshi da hakoranta yasa ya kunna wutan tareda maida kallonsa gareta domin yimata fada saiya tarar ta dunkulle guri daya.

Hatake yaji tausayinta yakamashi. Yamutsa fuska yayi tareda kashe A.C dakin, Yadauki bargo ya lullube taa.

---
TOH FAN'S KOYA ZATA KASANCE TSAKANIN KABIR DA AMRIYA.

COMENT PLEASE.□□□□
ALKALAMIN □□□?
BABY ISHA □□□□□□
2/28/24, 22:08 - AISHA M.B (Baby isha): □□ BISSMILLAHI RAHANI RAHIM □□

ALJANAR RUWA CE □□□□□□□□□□? PAGE 30

WRITTEN & DIRECTED □□□□ Y BABY ISHA □□□□

""""""

Kallon shi khaleed yayi yace Kama isa tare zamuje wlh mune mota  kokuma yanzunan nakira mom nasanar da itah halinda ake ciki

Toh shikenen mutafi cewar kabir futowa sukayi daga cikin hotel din suka bazama nemonta amma koh inuwanta bazu ganiba.

Tun kabir baya damuwa haryadawo yafara damuwa akai.

Nigeria

Wani hawaye mai zafi ne yakebin kuncita bude kofan taji anyi da sauri tashare hawayenta kallonta doct amina tayi tareda nufa inda take tadafa kafadan ta .

Tace doct safiya kina lafiya kuwa naganki cikin damuwa aka .

Kallon doct amina doct safiya tayi Tace bakomai .
Bakomai kuma naga kina kuka Dan Allah kifadamun meyafaru .

Share hawaye tayi Tace na aikata babban zunubi da Allah bazai taba yafemin bah . na aikata babban laifi a rayuwata ta duniya babu Wanda zai iya yafewa . tabbas naci amana ,nayi yaudara, no muguwa CE ,kwarai banida imani, tana kaiwanan ta fasheda matsanancin kuka,

Sosai hankalin doct amina yatashi Tace wane laifi kikayi da kikecewa Allah bazai taba yafemiki bah ,shin kinsabawa mijinkine ,Doct safiya Tace Aa kin yi kisan kaine , girgizamata kai takuma yi, doct amina takara tambayanta shin kin sabawa sharia musluncine ,shiru doct safiya tayi Tace inason zan nuna miki wani abune amma Dan Allah ki rikeshi a sirri banason kowa yasani.

Doct amina Tace menene nunamin.

Mika hannunta doct safiya tayi tareda nufa inda Jakarta yake  tadauko wani karamin box . tareda komawa inda take zaune Tace kinga wannan
Box din yakai shekaru 30 da yankai ajiye  kuma sbd zunubinda na aikata yasa na Adana shi sbd wancan azzaluman matan inason kobayauba gaskiy tayi halinta.

Doct amina Tace nifa bangane abunda like fada bah , wayan doct amina ne taji yafara ringing  daga wayan tayi tareda fadin gani nan zuwa ajiye wayan tayi Tace kiyi hakuri safiya abban Yusuf ne yadawo kuma yana son ganina gobe zaki cigaba barana taci .

Shikenen toh asauka lfy. Daukan Jakarta doct amina tayi tareda fucewa daga dakin .

Nannauyan ajiyan zuciya tasauke Tace ya Allah inason na sanarwa sanarwa wadanan ahali biyunan gsk amma nakasa ya Allah ka taimakeni natonawa wannan matan asiri.

Daga sama taji ance badai yatona nawaba saidai yatona taki asirin.

Bangare su kabir neman duniya sunyi amma basuga Amriya bah.

Sosai hankalisu takara tashi . wajan shaguna suka nufah sukafara nuna photonta koh sunganta amma bawanda yaganta

Itakam Amriya tana geden bakin titi tayi tagumi.

Manage PAGE pls
2/28/24, 22:09 - AISHA M.B (Baby isha): Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/JYYV16dbYaX1dykLX7EE91.

□□□□□□□□□€□□□□□□€□□□□□□€□□□□□□€□□□□□□€□□□□□□€□□□□□□€□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□?

BISSMILLAHI RAHAMI RAHEEM □□□□□□

ALJANAR RUWA CE □□□□□□□□□€□□□□□? PAGE 3 □□□ 1 □□□□□□ 3 □□□ 2 □□□
WRITTEN & DIRECTED □□□ BY BABY ISHA □□□□□□

---
Karasawa sukayi inda amriya take, Khalid yace Amriya menene kikeyi Hanan wajan,

Amriya tace Bb komi , Jan hannunta kabir yayi yace taso mutafi, tashi tayi, gaban kabir ne yafadi ganin yadda idanunwanta suka kada sukayi jajir.

Alamun kabir yamasu da ido, su sadiq na ganin aka suka wuce cikin hotel din.

Rike mai hannu amirya tayi gamm hawaye nabin kuncinta tace, meyasa kake son hallaka rayuwata ne, Eh Kalb, meyasa nake fuskantar tozarci da bakin ciki daga wajan kah, nuna saitin zuciyarta amriya tayi tace kasan yadda nakeji kuwa, jinake kamar na kashe kaina, Tana kaiwa nan ta fasheda kuka mai cin rai.

Karo na farko a rayuwarsa dayaga amriya tabashi tausayi, rungumeta yayi kam jikin jikinshi yace, kiyi hkr, namiki alkawari bazan sake miki abunda bazaki ji dadi bah kinji.

Dago kanta Tayi ta dora akan yatsansa, gabanta ne yayi mumunan faduwa, ganin babu zoben ta a hannunsa, cikin zuciyarta tace waiyyo Allah, zobena baya yatsan sa, yana wajan wa kenen, tunanin ta ne yatafi kan mom, tace tabbas wannan matar bazata bar kowa a Raye bah indai zobena yana wajanta, yakamata ace nakoma kafun ta aiwatar da mugun nufinta akan wannan ahalin ,

Kallonsa tayi tace Kalb, inaso mukoma gida, kabir yace kinaso mu koma gida karki damu gobe idan ma'aikatan dana tura zasuyi order na kaya suka kai saimutafi, amriya tace Aa Dan Allah yau mu koma, kaji,  kabir yayi murmushin yake yayi yace Tom shikenen,
Tareda sumbatar goshinta.

Saitin tureshi tayi Jikinta yafara karkarwa, hankalin kabir bah karamin tashi yayi ganin halinda amriya tashiga,

Ihuu ta kwallah, inda mutanen wajan suka zuba ido suna kallo,

Bah abunda bakinta kefadi sai ruwa, dukanta yayi chakk yanufi cikin wajan da itah.

Da sauri doct khadija ta juyo sannan tace, meyakawoki nan, murmushin mugunta mom tayi tace, abunda kike tunanin zai kawoni mana.

Nazone na karbi memory daga wajanki ,yana ina, doct khadija tace, baya wajena kuma meyasa zan baki,

Aba meyasa kika zama Mara imani aka, bazan kara aikata kuskure dana yi Ba abaya, har yau har gobe, saina tuna ranar dakika sani nayi kuskurenda bazan taba mantawa dashi bah.

Ke wace iriyar muguwa ce, kin kashe mutane bah iyaka, kin raba da da mahaifyarsa, kin mayarda mutane bayinki, tabbas zakiyi danasanin abunda kikeyi, wlh wlh, wlh, Saikin yi dana sani, a lckn da aka zo zaran ranki, a lckn zaki San irin kuna da azabar da zare rai yake dashi.

Hahahaha, mom ta kwashe da dariya Tana mai fadin kijira kinga abunda zai farudake tukun kafun kiyanke abunda zai farudani.

Kallon sauran yan qungiyan tayi tace inason yanzunan ku kimin ita fadata, daya daga cikin mutanen yace angama shugaba..

Direct daki kabir yakaita tareda kwantar da ita akan gado, tareda dauko inhaler dinta yabata tashaka , babu bata lck tasamu nutsuwa, ajiyan zuciya yayi yace,  na tambayeki, shin kinada aljanu ne koh shafar iska, Girgiza masa kai amriya tayi tace Aa,

Toh meyasa, kike yawan faduwa, kamar wata mai aljanu, gsk abunan naki akwai lauje cikin nadi.

Murmushi amriya Tayi cikin ranta tace Idan da kasan wahala da gwagwar mayar da nakesha wajan cetan rayuwarka da bazaka CE aka bah, tabbas yakamata, na koma sbd wannan azzalumar matar taruga tasaka wannan zoben ,

Kabir yace toh shikenen kishirya zamu koma yau, yana kaiwanan yafuce yabar mata guri.

Yana futa amriya, ta Rike kanta wanda yake mugun saramata, tashi tayi a daddafe tanufi toilet.

Chan cikin daji suka Shiga da doct khadija
Inda yan qungiya suka taru ,

Daddaureta akayi ajikin bishiya Wanda yan qungiyan suke kiranta da bishiyar bishiyar azaba.

Zama mom tayi, tace zan Kara tambayanki a Karo na karshe ina memory da bayanan nan suke,

Doct khadija tace bansaniba muguwa azzaluma mara imani, mai bushashiyar zuciya, Allah ya wadaran wannan rayuwa taki, tabbas bakiji dadin rayuwa bah,.

Kuma bazan Bari ki kara nasara akaina akaro na biyu bah.  na rante da Allah saidai ki kasheni, amma bazan fada miki inda yake bah.

Ran mom ne yayi kololuwar baci tace wato sbd kinga ban sakar miki azaba bah shiyasa kike baki koh, toh yanzu nan zan gama dake, idan yaso kya basu lbr achan.

Daukan wuka mom tayi, tafara tsaga cikin doct khadija, wani irin azzababbiyar kara doct khadija tasaki,

Zaki fadamin koh saina gama dake,  hawaye ne yafara bin kuncinta inda jini keta malala abakinta da cikinta, tace

Bazan fadaba, Kuma wlh, acikin yaranda kika bi kika mayardasu marayu, a lckn da basuji bah basugani bah, daya daga cikin su ita zata kawo karshenki, ki je kirubuta zakice nafada miki.

Murmushi mom tayi tace ba yau nafarajin aka daga irinku bah, kindauka zan rabudake nee Dan kinfadamin aka, toh shikenen tunda bazaki futoda memory bah, toh kingaishesu idan kinje.

Tana kaiwa nan ta soka mata wukan da karfi Chan cikinta har ya ratsa jikin bishiyar. Faduwa doct khadija tayi muttaciya

Daga wukan tayi tace ina bukatar jinin jariri yanzu nan , angama shugaba,

Akwaishe mun gawar wannan matar a jefa a cikin teku yadda kiyaye zasuyi abincin dare da namanta,  angama shugaba.

Hawaye ne yafara zuba a fuskan aunty amarya dake tsaye, cikin ranta tace tabbas matar nan shedaniyace, mara imani, wane sirri nee yake a memory, menene takeson doct khadija tabata, tabbas akwai lauje cikin nadi.

Alhj usman ne yace ranki shi Dade,  ga yata zainab tanaso ne tashiga qungiyan devilish,

Kallonta mom tayi tace, yarka CE, Alhj usman yace Eh yata ce, zainab tace ranki shi Dade nima inaso nazama yar qungiya na sha'ara yadda babu Wanda zaimin na Kyale,

Dariya mom ta kwasheda dashi tace karki damu indai zaki iya shan jini toh zaki zama yar qungiya, gobe ki hallarci taro, zaki zamo yar qungiya, kuma sannan dole ki sadaukar da abunda kika fiso,

Zainab tace komai zan iya bayarwa indai har zan kasance a wannan qungiyar .

Tashi mom tayi tace, yanzu kowa zai iya tafiya, yau karku manta kowa yasha jinin akuya, sbd jikina na bani akwai wani iftilahi dake shirin faruwa kwanan nan .

Angama uwar shedanu,

Watsewa kowa yayi daga wajan, inda aka dauki gawar doct khadija aka jefata a ruwa kamar yadda mom ta umarta.

Shiryawa  su kabir sukayi tsaff, inda suka
Nufi Airport,

Daukan Wayanshi sadiq yayi, yayi dialing number Nadira ringing biyu ta dauka, Tareda yin sallama, , amsawa yayi yace, my wife to be ykk, murmushi nadira tayi tace Lfy lau, kaifa, sadiq yace ina cikin koshin Lfy kamar yadda kike.

Alhmd Nadira tafada, tana mai fadin wlh Nayi missing dinku yaushe zaku dawo, sadiq yace yau dinnan da yardar Allah.

What, ta tashi a kwance datake tace are you for real, gsk naji dadi sosai,
Shine Kuma baka gayamana bah, murmushi sadiq yayi yace, yanzu dai nafada miki kohh,.

Tom shikenen Allah yadawo daku Lfy, sadiq ya amsa da ameen .

Sadiq yace yanzu jirgi zaitashi, saimun Iso koh, Tom shikenen, ka kulamin da kanka, kabir yace insha Allah, kema ki kulanmun da kanki kinji.  Tom Nadira tace, daganan sukayi sallama.

Kashe wayan nadira tayi Tareda saukarda nannauyan ajiyan zuciya,

Su Ummi dake Zaune suna Kallon ikon Allah Tace ohh wayaga su aunty nadira da soyayya, kamar bah da bah dakika mutuwar son yaya kabir. Yanzu Kuma Gashi, yaya sadiq zaki aura, inda Allah ke ikonsa kenen

Murmushi Nadira tayi tace

□□□□□□□□□□□□□□□□□□
---
□□□□□□□□□□□□□□□□□□

COMMENT & SHARE □□□□□□

ALKALAMIN □□□□□□□□□□?
BABY ISHA □□□□□□(AISHA M.B)
2/28/24, 22:09 - AISHA M.B (Baby isha): Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/IhGI6IqdpVVABEzyBe7LGM

□□□□□□□□□€□□□□□□□€□□□□□□□€□□□□□□□€□□□□□□□€□□□□□□□€□□□□□□□€□□□?
□□□□□□□□□□□□□□
□□□□□□□□□

□□ Bissmillahi rahamani raheem □□

ALJANAR RUWA CE BOOK 2 □□□□□□□□□□□? PAGE 3 □□□ 2 □□□□?3 □□□ 3 □□□

WRITTEN & DIRECTED □□□□□□□□□□□?
BY BABY ISHA □□□□□□

---

Murmushi nadirah tayi tace Allah ya ruga daya kaddara cewa bani zan aureshibah, banice na dasawa kaina sonsa bah lkcn danace inason yahya kabir, idona yarufene akansa, kuma yanzu Allah yabani mafi alkhairy, kuma gashi yahya sadiq dinmah ya Maye gurbin yahya kabir .  Kuma naga aibakwa sonsu aka baku.

Gabadayansu sukace mezai hana musosu, saidai fatima da Aka bawa yahya khaleed .

Yamutse fuska fatima tayi tace nifah Allah yahya khaleed inba biyayya iyaye bah bazan aureshibah. Tunda sukatafi koh kirana baitaba yibah ,sai shegen jijidakai jaraba ni nama rasa da yahya kabir da shi wanne yafi jijidakai.

Aba kema kinsan yahya kabir yayi gaba wlh cewar nadirah.
Toh  susuka sani wlh koh ajikina

Nadirah tace Yanzu tsoro na daya nee, shine kada agano cewar amriya bah mutum bace shine kawai tsoron danake jii.

Dan jimm gabadayansu sukayi  Fatima tace wlh abunda nima nake tsoro kenen sbd idan akasani most especially yahya kabir zai iya saa a kulleta a gidan yari.

Insha Allah mah akan bazata faruba cewar kalisat.  Tashi Ummi tayi tace kunga bah zama yakamta muyi bah kunsan yau zasu dawo muje mufara shirye shirye.  Oh akane fah kunga kutashi muje.

Tashi sukayi inda sukafara gyara gidan.

Kalisat dakuma nadirah suka nufi kitchen sukafara shirye shiryen girki.

Saida suka dau 1:30 minutes sannan suka gaba komai dakomai .

Dakinsu triplet salma tashiga tace sufuto abinci yayi ready. Gamunan zuwa cewar adeef.

Bayan tafuto tanufi dakinsu mom tace angama lunch food. Mom tace kee malama dallah fuce kiban guri.

da mamakin ta ummi tace Mom meyafaru kuma me aka miki Dan Allah mom idan nice namiki laifi kiyi hkr ki gayamin zan kiyaye gaba.

Kallonta Mom tayi sannan ta buga murmushi yake tace sorry ummi wlh damuwa ce tasani yimiki ihuu kinji. Shikenen mom ,fucewa tayi daga dakin sannan tanufi dakin aunty amarya.

Bayan fucewar ummi mom tayi dariyar mugunta sannan tabude drower tadauko wani dunkullalen magani. Tareda juyashi a hannunta tace yanzu aka soma wasan.

Saina kasheku gabadaya sannan dukiya gidanan yazama nawa na ni kadai. Futowa tayi daga dakin ganin bah kowa a parlour yasata nufah dining inda kuloli na abinci ke jere akai.

Kallonsu tayi tareda bude abinci gabadaya tafara barbade abinci da guba . Sannan tayi saurin rufeshi.

Ammi kiyi hkr kidaina kuka Dan Allah banajin dadi, yanzu daga yin mafarki saiki tashi kina kuka,  kallonsa tayi tace aba yusuf yanzu wajan shekara 20 kenen da yan kai,  bah ranar dazata tashi tafadi banyi mafarkin yata bah. Jikina yanabani cewar yata tana raye

Ammi kinayi mafarkinne sbd kinsa abun aranki, babu inda mutacce yake dawo duniya wai yacigaba da rayuwa.  Gashi inason zuwa wajan aiki ankawo case wanda zan gabatar gobe a kotu. Yanzu taya zan iya zuwa kina kuka.

Daddy Dan Allah kashawo kanta. Dago kai daddy yayi yace yusuf nikam mezance .

Nace mata mu fauwala wa Allah komai, ba ita kadai take jin kunci bah nikaina mah aka, so mezanyi . Yanzu gashi har B.P ne da itah

Kuma at anytime idan tacigaba zai iya zama high.  Yusuf kawai kaje wajan aikinka nizan rarrashi abata ba kaiba.

Maza maza ka wuce kaje. Amma daddy bazan iya tafiya bah batareda naga tadaina kukan bah.

Ni dadi nadai taurin kai nace maka katafi koh i know what am saying. Okay daddy shikenen zantafi amma ka tabbatar kasata farinciki, kuma kasa taci abinci. Never mind.

Fucewa yusuf yayi sannan ya shige mota dafa kan tyring motan yayi wani hawaye mezafi nabin kuncinsa.yace Allah sarki kanwata , Allah yajikanki da rahama. Share hawayenshi yayi yatada mota sannan yafuce daga gidan .

Bayan fucewarshi  daddy ya tashi yaje kusada ammi tareda rike hannunta yace. Aba my ameenatuwa kiyi hkr kidaina kuka. Kinji adua yakamta mudunga mata bah kuka bah, kinji.

Ammi tace nikasakeni nayi kuka naa, aba my dankalin Hausa, kinsan mena tuna ranar auren mu dakika sha asha ado da dambareren jambaki, sai kika zama kamar indon kauye

Dariya manya ammi tayi tace kafara kohh, nace kadaina tsokanata , Aa nibazan daina bah har lckn wata mata tamiki gira wanda daya yayi hanyar arewa daya kuma yayi kudu

Hatare suka kwashe da dariya gwani sha'awa, share fuskanta ammi tayi tace kaiko meyasa koda yaushe idan ina cikin bakinciki saika San yadda zakayi kasani farinciki gsk kaidin na mussaman nee.

Daddy yace kwarai kuwa nidin na mussanman nee aii sbd ni nakine kema tawace.

Dan aka tashi muje muci abinci.  Aa nibazanci bah.  Masha Allah kenen yin kishiya a gidanan babu fashi kenen yafada cikin zolaya. Aba my chief Ni banaso cewar ammi,

Toh tunda bakya so kitashi muje muci kinji.

Tashi sukayi cikeda kaunar juna .

""""""""""""""""""""""""""""""""""

Jin hana kwankwasa kofa yasa Nadira tashi tanufi kofa tareda budewa. Ganinsu kabir nee yasata farinciki sannan tafara kiran sauran hatare gabadayansu suka iso, rungume amriya sukayi . Sosai kowa yayi farinciki da dawowansu,

Idan bangare guda kuwa ma'akata suka fara shigo da akwatuna dozen dozen da kayayyaki . Sannan suka shigardasu ciki babbar daki na ajiya suka tafi.

Futowa Mom tayi tace wow my son kundawo lfy. dasauri kabir yaje ya rungumeta sannan yace i really Miss you mom.

Murmushi mugunta tayi tace aba son yaushe kuka tafi da Jataka fara missing dina takarashe maganar tana kallon amriya. Idanuwan amriya ne yasauka akan yatsan Mom wanda zobenta ke sanye ajiki.

Sai a lkcn gabanta yakara faduwa . Tace kindai rantse saikin GA bayan wannan ahalin toh wlh muzuba mugani Allah bazai baki damar cimma mummunar manufanki akan wannan ahalinbah

Sakin Mom kabir yayi yanufi wajan aunty amarya yagaisheta sosai aunty amarya taji dadin dawowansu,

Itama amriya batayi kasa a gwiwa bah tanufi wajan aunty amarya sannan ta gaisheta, sosai aunty amarya ta tarbeta hannu bibiyu.

Aka gabadayansu sukafara gaisawa da juna cikeda kaunar junansu.

Mom tace yata amriya bah fada maiyakawo gaba, nibakizo kingaisheni bah aii. Cikeda jin takaici ta tashi tanufi wajan mom,

Sannan ta gaisheta tah. Kallonta Mom tayi cikin kasa da murya tace yakika ga salon nawa.

Murmushi amriya tayi tace yayi kuma aciki harda Nasaran daukan zobena dakikayi, kisani cewa wahalar da kanki kawai kikeyi bah wani abuba, irinku kamata ai ace kutsaya kuna tallah goro a kasuwa. Jin zafin maganar amriya Mom tayi har makogaronta.

Grandma tace haryanzu Baku gama kusun kusun dakukeyi bah. Murmushi Mom tayi tace grandma kinsan tsakani ya da uwa sai Allah. Yanzu bah wannan bah kutashi kuje kuci abinci.

Kabir yace okay mom baramuje mudan watsa ruwa muyi sallah.

Tashi gabadayansu sukayi inda suka nufi part dinsu .

Bayan sungama komai da komai suka nufi hanyar dining.  Daidai lkcn itama amriya tafuto daga part din aunty amarya.

Zama gabadayansu sukayi inda mom tafara bude musu abincin. Kallonta Khalid yayi yace Mom ke bazaki ciba,  mom tace eh wlh nakoshi,

Kallon abincin amriya tayi taga tabbas abincinan  an zuba guba aciki. Murmushi amriya tayi cikin zucinyata tace kindai dage saikin ga bayan wannan ahalin

Serving dinsu gabadaya mom tafarayi idon kabir ne yasauka akan yatsan Mom wanda zoben amriya kesanye yace Mom dama zobenan na wajan ki , eh wlh yana waje na sanda naje dakinka naganshi akan table,  nima kuma zoben na burgeni shiyasa nasaka kafun ka dawo , kabir yace amma naji dadi dakikasa sbd idan kikasa kamar nasaka nee

,Daukan chokula gabadayansu sukayi tareda yin adua suka tsokala chokali zasu faraci .

Ku dakata sukaji amriya tafada, da kallon mamaki gabadayansu suke binta dashi.

Sadiq yace amriya meyasa zakice mu dakata,  amriya tace zakusan dalili, tashi tayi tareda daukan wani plate din tazuba abinci sannan tasa agaban Mom tareda daukan chokali ta ajiye agabanta.

Amriya tace aba Mom dinmu taza'ayi kina matsayin uwa agidanan bazaki ci abinci bah, ke yakamata ace kinfaraci.

Murmushin yake Mom tayi tace ai idan kunci kamar nacine, ni naruga danaci.  Amriya tace amma yadda nagani shine wannan bai nuna cewa an iba bah tabbas baki ci bah.

Kinsan bamuason kisamu ulcer kinji Mom,  kici kinji.

Aba amriya Mom tace fah takoshi muci kawai cewar sadiq.

Babu wanda zaici abincinan, dawani irin jin mamakin jin kalamanta grandma tace ohh ni halimatu sadiya shin amarina fadamana dalilin dayasa bazamuci abincinan bah.

Mom kuwa ranta indan yakai dubu yabaci . Amriya tace dalilina shine wannan abincin akwai guba acikinta.

Hatare suka ada baki wajan cewa guba kuma, nadira tace meyasa zamu saka guba amriya, wlh bamusa guba bah.

Amriya tace nasan baku  bane kukasa, amma Mom tasani.

Zaro ido Mom tayi tace nikuma amriya sbd me zanyi kokarin cutarda iyalina, sune fah komai nawa takarashe maganar hawaye nabin fuskanta. Kuma tunda Baku yarda

danibah zanci abincin daukan chokali tayi zataci abincin, dakatarda itah kabir yayi yace Aa Mom kiyi hkr Dan Allah, ba abunda zaisa mu zargeki

Dan aka babu abunda zai hana muci abincinan.  Babu wanda zaici abincinan, aba amriya hankalinki guda kuwa yara susha wahala dafamana abinci kuma kice bazamu ciba grandma takarashe maganar taja chokali zata faraci.

Ganin akan yasa amriya barar da abincin gabadaya sannan ta dauki plate daya na abinci ta fuce waje.

Ganin abun nata bana sawa ido bane suka bi bayanta.

Bude daya daga cikin karnukan gidan tayi tabashi plate na abincin yafaraci, tsayawa gabadayansu sukayi suna kallon ikon Allah.

Aikwan ba'a fi ten minutes bah wannan karen yafara kururuwa yafara futa hayyacinshi jini yafara futowa tabakinsa da Ancinsa.

Zaro ido gabadayasu sukayi cikin tsoro da fargaba, basu ankarabah karen ya fadi a wajan mutacce.

Amriya tace dabba kenen shiyaci abincinan  ya mutu da kunci kuma aka za ku mutu,

Kallon Mom aunty amarya da amriya sukayi , hada ido sukayi su uku batareda kowa ya lura dasubah.

Kabir yace tabbas wanda yasaka gubanan yana cikin gidanan kuma dole aganoshi.

Amriya tace bah bukata domin ni naruga danasan wanda tasaka guban nan , zaro ido Mom tayi.

□□□□□□□□□□□□□□□□□
TOH FAN'S ANAN ZANDAKATA,

COMMENT & SHARE PLEASE □□□□□□□□

ALKALAMIN □□□□□□□□□□?
BABY ISHA □□□□□□
2/28/24, 22:10 - AISHA M.B (Baby isha): Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/DzIj6Y6KObvD2Bcmg8azU5

□□ Bissmillahi rahamani rahim □□

ALJANAR RUWA CE □□□□□□□□□□?

PAGE 3 □□□ 3 □□□□□□ 3 □□□ 4 □□□
WRITTEN & DIRECTED □□□? □□□□□□□□
BY BABY ISHA □□□□

---
Hatake Mom tarike hannunta wanda zoben ke sanye tafara jujuyawa, chak gabadayansu suka kame guri daya banda amriya wacce ke tsaye tana kallon ikon Allah.

Kallonta Mom tayi tareda manna mata ido daya, sosai ran amriya yabaci, tace ke azzalumar mata maza kida wodasu hayyacinsu inba aka bah zanuna miki fushin aljanar ruwa,

Dariya ta kwashe dashi tareda fadin ke nan a tunaninki zaki iya tonamin asiri nee impossible, toh barana fada miki koda kinfada musu bazasu taba yarda dake bah, kuma kitsaya kigani agabanki zan kashesu.

Karya kike, wlh indai ina raye bazaki ci galaba akan wannan ahalin bah, wai laifin mesuka miki da har kikeson kiga bayansu,

Babu ruwanki Cewar mom , dole na kashesu most especially kabir idan ban kasheshi bah qungiya bazata dorani akan gujerar sarauta bah na qungiya Dan aka matsa chan yau dinan zankashesu.

Saboda wani banzar kujera kikeso hallaka kowa toh wlh indai har saikin kashesu ne zaki samu kujera toh wlh kin sa a ranki kin rasa.

Haaaaaaa ta kwallah wani ihuu wanda yasa komai na gidan yayi sama, tafarayin gurnani kamar kura.

Murmushi amriya tayi tareda rintse idonta hatake wani brown din aske ya bayyana, bude idanuwanta amriya tayi tadora akan na Mom dake shirin hallaka kabir.

Babu bata lck takamo wuya Mom tareda shaketa,  tareda daga ta sama ta fara juyata ta jijigata, sosai Mom ta jigata, cillar da ita kasa amriya tayi,

Amriya nasakin ta Mom tafara tari tareda kallo amriya tace ni zaki yiwa aka, tabbas kin kuna wutan dafa kanki wlh duk wanda yayi dani uwar shedanu bana barinsa a raye, tana kaiwa nan ta bace.

Ba bata lck su kabir suka dawo hayyacinsu,  kallo amriya nadira tayi tace amriya meyafaru, meyasa muka futo waje,

Amriya ta bata amsa dacewa babu komi mushiga ciki, gabadaya ciki sukashiga

Babu wanda yatuna komai acikinsu,

Washe gari
Ummi ce hannunta rikeda plate da bawon lemo a hannunta tana tafiya tana yan wake wakenta

Hajiye plate dintayi tareda zama tafara bare lemon domin tasha, kwatsam kuma saitaji kukan mutum daga gefe

A tsorace ta tashi tareda nufa inda takejin kukan tazo zata murda handle din kofan taji andafata,  a tsorace tajuyo

Ke ummi mekikeyi hanan wajan, wlh amriya ina zaune kawai naji kukan mutum shine nace barana duba waye yake kuka

Toh shikenen nasan mah babu kowa kije aunty amarya tana kiranki kinji, tom shikenen barana tafi cewar amriya.

Amriya naganin ummi ta tafi ta bude kofan , wani hayaki ne ya buso mata kmr lckn baya, kaucewa tayi,

Kallon dakin tayi taga duhu sosai ko yatsunta bata iya gani,  magana tafarayi kamar aka waye, wanene Hanan, waye yake kuka.

Still ba'a amsa mata bah, hannunta ne yayi nasaran taba socket na kunna wuta, babu bata lck ta kunna wutan dakin Hatake wuta ya baiyyana,

Zaune take ta chunkushe guri daya kanta a tsakanin cinyoyinta gefe guda kuma  jikinta yana zagaye da kachochi inda gashinta wanda yake da tsayi yayi fari da datti,

Amriya batayi kasa a gwiwa bah takarasa wajan matan tareda fadin wacece kee meyasa kike hanan wajan waya miki aka kifadamin namiki alkawari zan taiamaka miki.

Ture amriya matar tayi hatake tafadi.

Tana mai fadin kibar nan kitafi, banaso, bana bukatar taiamakonki, kitafi, karki sa rayuwanki a atsari na rokeki kitafi tana Kaiwa nan ta fashe da matsanancin kuka mai cin raii.

Sosai amriya bata ji dadin ganin matar nan acikin wannan halin bah, batayi kasa a gwiwa bah takara nufa wajan matar,

Dakatarda ita tayi tareda fadin kada kimatso kusada nii, na gayamiki banaso kitafi nace kije bana bukatan taimakon naki, wlh banaso.

da sauri amriya ta isa wajan matar tareda rike hannunta hawaye yafara Bin kuncinta tace Dan Allah na rokeki kada ki koreni kigayamin wayamiki aka, kuma sannan kedin wacece mekikayi da har kika cancanci a wulakantaki ta wannan hanyar.

Nuna jikin bango matar tayi, kallon inda take nunawa amriya tayi, photo ne wanda wata mata da DAD sukayi.

Amriya tace wannan kamar DAD nake gani, matar tace shine wacce take kusada shi nice,

dawani kallon mamaki amriya ta kalleta tareda fadin taya aka zata kasance , kwarai kuwa nice shidin mijina nee.

Azabure amriya ta tashi tace wannan karyan banza nee DAD bashida wata matar, mata biyu nee dashi ,aunty amarya dakuma Mom.

Kallon amriya matar tayi tace wannan matar ta cutardani bah adadi ta azabtar dani bah iyaka, kuma sannan takeso ta kashe dana Dan Allah kada kibari ta cutarda dana ,

Cikin rashin fahimtar maganta amriya tace danki kuma waye danki, jinkaran tafiya yasa matar ture amriya,
tareda cemata ta futa

Kifuta, Dan Allah kitafi, amriya tace taya zantafi batareda kingayamin waye danki bah kuma waya miki aka,

Nace miki ki tafi koda nafada miki babu abunda zaki iyayi akai Dan aka kitafi bana bukata,

Amma dan Allah kifadamin,. Kitafi bana bukata matar ta daka wa amriya tsawa, babu bata lck amriya tafuta daga dakin.

Hatake kofan dakin ya rufe kansa, barin wajan amriya tayi tanufi dakin aunty amarya,

Tana shiga kuwa tayi sa'a babu kowa a dakin sai aunty amarya zuwa kusada ita amriya tayi tace aunty amarya, dago kai aunty amarya tayi tace laa amriya kece dama yaushe kika shigo,

Aunty amarya inason namiki wata tambaya, toh amriya Allah yasa nasani,

Amriya tace shin kafun keda Mom DAD yataba yin aurene , aunty amarya tace yes of course mana, bana fadamiki bah sunanta fatima amma a garin haihuwa ta rasu shima danda ta haifa yabita.

Amma meyasa kike tambaya, girgiza Kai kawai amriya tayi tace bakomai kawaidai inason nasani nee. Barana jee cewar amriya.

Fucewa tayi daga daki tareda tambayar kanta cewa toh tunda fatima ta rasu wacece ita wannan toh.

Bah tsanmani taji ankira sunanta juyawan dazatayi saita ashe DAD ne, gabadaya kowa na family Suna zauna da alaman ita ake jira .

Amsawa tayi tareda gaisheshi tace trudge kadawo DAD, murmushi yayi yace jiya daddare na dawo lkcn dana dawo Mom tace mun kunyi bacci shiyasa bantasheku bah.

Okay Tom DAD andawo lfy, lfy kalau yata dama mgn mai mahimmanci zamuyi kuma kema tashafe kine kinji Dan aka samu guri ki zauna.

Kmr yadda dad ya umarta aka tasamu guri tazauna tana facing din Mom, inda Mom ta galla mata harara.

Itakuma amriya takauda kai, gyara muryansa DAD yayi yana mai fadin dalilin da yasa kukaga na taraku shine, nida Mom dinku mun yanke hukunci cewa  wannan sati Mai zuwa idan Allah yakaimu kabir dakuma Khalid da sadiq za'a daura muku aure. Yanzu yasa zan tambayi ra'ayinku gameda hukuncin dana yanke.

Damm dammm damm gaban amriya yafadi.

Zaro ido kabir yayi tareda mikewa tsaye yace DAD cikin satinan ina laifin nan da watanni, yanzu idan mukayi auren ina zamu zauna

DAD yace tambayata kakeyi duk uban gidajen da kakedasu bazaka iya daukan daya kuzauna bah, DAD nidai gsk noo am not ready for this marriage.

How dare you DAD yafada ranshi a bace, yace wlh kabir kafuta idona babu wanda yayi complain saikai dinan ,meyasa toh wlh tunda kace aka mah jibi jibin nan za'a daura auren. Kuma a gidan nan zaku zauna inyaso ka hadiye zuciya ka mutu

Zaro ido gabadayansu sukayi , Khalid yace dad please kada ayi aka Kalli amaren namu koh gyara fah basu faraba , abubuwan nan de na mata duk basuyi bah, kuma ni harga Allah amarya bazata zomin gida tana doyiba,

FATIMA ta karbe mgn dafadi mu dama kodayaushe a gyare muke wlh babu wani doyi idan bazaka iya bah sai ka barmata Gidan kanemi wani,

Ke ni sa'anki nee wlh zan tsinka miki mari, ni baruwana danke zan Aura wannan bata shafeni bah duka zakici wlh,

Ya isa,  Mom tafada yanzu ku dan tsabar rashin kunya irin naku muna nan wajan kuke chachan baki wlh zan sabawa mutum.

Kuma hukunci da aka yanke shine sati mai zuwa za'a Daura aure kafunan an gyara muku amarenku bah aka kukeso bah.

Kallon amriya DAD yayi yace amriya niba mahaifinki bane banida iko akanki hakkinki zan barki ki yanke hukunci da kika ga yafi miki idan kinga bakyaso wannan auren kada kiji kunya kifadamin.
Bazan taba jin aushiba kinji, Dan aka gobe washe gari kowa zai hallara zaki fadamin ra'ayinki kinji.

Girgiza Kai kawai amriya ta iyayi,  bayan kowa ya watse kabir yaje wajanta yasameta yace ke kada ki kuskure kice kin amince kinji nafada miki, ni banasonki ina da wacce nakeso idan na aureki kamar na ci amanar ta,  kinajina ita kadai zan aura ba keba,

sbd ita ta bada rayuwanta domin ni na rayu, ita ta taimakamin lckn da rai a hannun Allah meyasa bazan saka mata da alkhairy bah kinajina bah rokonki nakebah gargadi nake miki.
Yana kaiwa nan yayi fucewarsa.

Washe gari kamar yadda DAD yafada kowa ya hallara amriya kawai ake jira,

Yata amriya ina jinki fadamin hukuncin da kika yanke, kallon kabir tayi inda taga ya daga mata gira daya, tareda mayarda kallonta kan DAD tace na amince da wannan auren

Zaro ido kabir yayi yana mai jin takaici da bakinciki,

Wow my daughter ina Alfa'ahari dake gsk kedin daya ce acikin dubu.
Watsewa kowa yayi.

Bayan kwana biyu
.
Ba'a dau lckn bah aka fara gyara amarenan guda uku, inda sukeshan gyara bah kadan bah, gabadaya gida mutane suncika , ita kanta mami ba'a barta abaya bah, sosai mutane kala kala daban daban,

 wanda bakayi tsammanin zuwansu bah suka hallara hatta mahaifiyar sadiq, Aisha dakuma khadija,  saikuma doctor amina wacce itama tasamu gaiyyata daga aunty amarya
.

Aka, aka dunga durka musu magunguna hana yimusu turaruruka wanda mami tayi hodansu daga sudan.

Sosai su amriya sukasha gyara hatta lalle kitso anyimusu.

Yau takama ranar dinner na biki, gabadaya kofan gidan yacika da motoci kala kala bah adadi, idan ka gani zaka dauka koh bikin govnor akeyi,

Wow amriya kinga yadda kikayi kyau kuwa wlh kinyi kyau bah kadan bah, murmushi amriya tayi tace nadira kenen kema kinyi kyau aii . Fatima tace kunga muje kunga mu amare ake jira,

Masha Allah nace idan gabadayansu suke sanye da Arabian gown kala iri daya, babu abunda ketashi ajikinsu sai kamshi.  Sosai sukayi kyau , ba kamar amriya wow so cute kamar yar Indian. Hannunsu sanye da handbag Dan karami sai takalmi Hills mai kyau,

Hatare suka futo daga dakin sukanufi hanyar waje hatake wanda suke parlour suka maida kallonsu kansu. Sukafara guda suna tafi

Sosai kowa ya yabi kyau dasukayi kyau barima amriya, duk tacinye wankan.

Kallonsu doctor amina tayi tareda rufemusu fuskoki da mayafi,  tace yarana kunga yadda kukayi kyau kuwa gwanin sha'awa,

Zuwa Aisha tayi tace wow kunga yadda kukayi kuwa kamar wasu triplet,  fatima tace zaki fara kenen kohh,,

Khadija tace Dan Allah kutawo maza jenku duk ku suke jira fah kuma kunsan halin yahya kabir tafiya zaiyi wlh.

Shikenen bara mutafi koh

Suna futowa kowaccensu tanufi cikin mota wanda suke hajere guda uku bakake biyu na tsakiyan fari.

FATIMA da nadira sukanufi bakaken itakuma amriya tanufi farin motan shiga kowannensu yayi banda fatima dake tsaye tana jiran Khalid yabude mata kofa.

Tacikin motan Khalid yace ji wannan jiratake nabude mata kofa koh chabb kina ruwa wlh,

Gani bashida niyan bude mata yasata bude da kanta tashiga,

Hatare motocin suka bar arabar Gidan,.

Sauran su ummi kuma suka au sauran motan suka tafi suma.

Kallon amriya kabir yayi yace ke bude fuskanki, bude mayafinta tayi cikin zucinyanshi kuwa yace bah laifi tadanyi kyau,

Wato kee nace miki kice bakyason auren shine kikace kinaso koh,  murmushi amriya tayi tace. Eh mana inaso kuma kaima kanaso.

□□□□□□□□□□€□□□□□□□€□□□□□□□€

Amriya jin zuciyanta tayi kamar kama da wuta tsabar zafi da kuna dakuma radadin da takeji.

Fucewa yayi yabarta ita kadai adakin.
Tana ganin yafuta, ta fashe da matsancin kuka, tareda nafadi na aikata kuskure tabbas nayi danasani, nashiga uku saura kwanaki kalilan da gurmuzu ya gindaya min zan koma teku idan kuma ba aka bah zan mutu,

Ya zanyi kenen na roke ka Kalb kabani zobena, tafada hawaye nabin fuskanta.

Tacigaba dafadin menene anfanina kenen, meyasa ma lkcn da iyayena zasu mutu basu mutu tareda niba, nagaji nagaji, amatsayina na aljanar ruwa babu abunda zan iya tabukawa meyasa, sbd me, meyasa nayi sanyi aka.

Tana cikin magana nee idanuwanta suka sauka akan zobe akan table, zaro ido tayi tace zobena, saurin dauka tayi tareda jujjuyashi rungume zoben tayi, hawaye na zalalo wa.

Kallon zoben tayi tace a yau dinnan babu wanda zai hanani zuwa duniyata.

Jin tafiyan mutun nee yasa tayi saurin komawa tareda kwanciya akan gadon tayi luff.

Bayan futowarsu doctor amina daga dakin amriya , dad ya adawa doctor amina goma na arziki, da murnanta ammi ta karba tareda yimusu Godiya.

Inda shikuma yusuf wajan dinner ya haduda salma wato kanwar kabir , lckn daya tashiga ranshi, babu bata lck yasameta inda sukayi exchange din number.

---

Shigowa kabir yayi da ruwan swam water tareda inhaler dinta dakuma magani mika mata yayi yace karbi kisha yafada yana yamutse fuska.

Kauda kanta amriya tayi tace banaso banashan magani,
Ni bashi nakeso bah Indo kadafa min ruwan zafi zanyi wanka sbd inajin zazzabi.

Jin maganarta yayi kamar saukar aradu, kallon sama da kasa yayi, sannan yakalli hagu da damansa yaga baiga kowa bah, sannan yamaida Kallonsa kanta

Tareda nuna kansa da danyatsa yace wai kina nufin nii kabir, shagwaba fuska amriya tayi tace toh inbaka min bah wazai min.

Wani kallon tara saura kwata ya watsa mata sannan yace are you for real. Kina nufin nii,

Na dafa wa mace ruwan wanka, murmushi yayi yace toh barakiji idan magani kika sa abaki toh maza maza kikoma wajan bokanki kice masa bai kamani bah, kuma bazai kamani bah, rubbish, yakarashe maganar tareda jan tsaki.

Jikin amriya nee yayi sanyi nan kuma ta Tuna da irin shawarar da su aunty amarya suka bata,

Kuma yatsine fuska tayi tace nidai wlh kadoramin kokuma washe gari nafada su mom cewar munyiii.....

Munyi mee eh, ke banason shashanci fah karba kokuma in dauko bulala jikinki yayi tsami.

Karba tayi tasha sannan ta kwanta inda baccin barawo yasaceta. Shikam gogon sai kallonta yakeyi,  murmushi kawai yayi yace well she's not bad. Yana ganin bacci ya kwasheta , yatashi tareda nufa dayan dakin wanda yake nashi, ya kwanta

Washe gari, sosai Jikin amriya yakara tsananta abun ba'acewa komai lokaci daya ta rame.

Sosai hankalin aunty amarya da sauran yan gidan yatashi

Aunty amarya tace ke salma wai meyafarune, salma tace aunty wlh dama grandma ce tace nakawo musu abinci breakfast bayan nakaiwa su nadira shine sai naganta ayashe akasa, wlh aunty tsoro nakeji.

Gabadaya fuskokin kowa babu alamun farha kana ganinsu kasan sunacikin tashin hankali babba.

Jin muryar amriya sukayi tana fadin ruwa, ruwa, inason zanshiga ruwa .....

MANAGE PAGE PLEASE □□□□□□

COMMENT & SHARE □□□□□□

ALKALAMIN □□□□□□□□□□?
BABY ISHA (AISHA M. B) □□□□□□
2/28/24, 22:11 - AISHA M.B (Baby isha): Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/JYYV16dbYaX1dykLX7EE91

BISSMILLAHI RAHAMANI RAHEEM □□
□□□□□□□□□□□□□□□□□

□□□□□□□□□€□□□□□□□€□□□□□□□€□□□□□□□€□□□□□□□€□□□□□□□€□□□□□□□€□□□?  □□□□□□□□□□□□□□□□□□

ALJANAR RUWA CE □□□□□□□□□€□□□□□? PAGE 3 □□□ 6 □□□□□□ 3 □□□ 7 □□□

WRITTEN & DIRECTED □□□□□□□
BY BABY ISHA □□□□□□

---
Gradma tace oh ni halimatu  yanzu yaronan sbd Rabat kai azzalumini nee,  daga kai yarinya jiya jiya jiya sai ace kai mata wannan aika aikan.

Kabir yace ban fahimci inda kika dosa bah, gradma tabashi amsa dacewa ai bazaka fahimta bah toh karkade kunnuwanka kajini, wlh idan aminiya bata samu Lfy bah toh sainakai ka kotu

Doctor Amina da aka kirace Tafuto daga dakin tace alhmd yanzu dai mara Lfy tasamu bacci, kuma  naga alamun kamar tanada asma kuma is critical yakamata adunga bata magunguna akai akai if not she may lose her life.

You guys should be very careful,  and na aje mata magani zata shashi Kuma ku tabbatar kunbata wannan maganin, please and please.

Nadira tace insha Allah doctor Amina zamu kula, okay doctor amina tace tadauki jakarta tanufi hanyar waje kamar ta tuna wani abu kuma saita tsaya,

That's remind me, mom, dago kai mom tayi tace na'am, doctor amina tace i think there is something special about that's girl, tabbas akwai wani baiwa tattareda ita,

Hatake ran mom yakara bacci takara hassala danne fushinta tayi tasaki murmushin takaici tace kwarai kuwa kinga nayi sa'ar samun suruka tagari kamar amriya

Murmushi doctor amina tayi tafuce daga wajan, Tana fucewa itama mom tayi part dinta.

Suko sunadira suka koma part dinsu inda aunty amarya da kawarta maimuna suka dunga dura musu magunguna da turarruruka Kala kala, gabadaya gidan kamshi  umra kawai kakeji da kamshi turaren wuta.

Part din amriya suka koma inda suka tasheta Tasha maganinda doctor Amina tace Tasha . Inda suka sata a gaba ta dunga durkan magunguna datayi order daga Niger

Suka turare ko ina na gidan bah abunda ke tashi sai kamshi. Tareda daukan breakfast dinta aunty amarya tace taci, amriya tace takoshi.

Hade rai aunty amarya tayi inda tasata agaba tafara feeding dinta da kanta.

Bayan fucewar doctor amina ta kwasheda dariyar mugunta tareda daukan wayanta tayi dialling number ,ringing biyu aka dauka.

Daga dayan bangaren mom tace you did a very good job zainab, murmushin mugunta tayi Tareda cire mask din datasa a fuskanta, Wanda yayi suffar doctor amina, zainab tace ai babu wacce tadace da kabir samada ni din nan.

Amma fah mom kin iya basaja, yanzu step 1 na kammalashi saura step 2, ina mai tabbatar miki cewa tanashan wannan magani toh bazata kara ganinta awanan duniyar bah saidai  duniyan.

Mom ta kwashe da dariya tace hmm dama nafada mata Duk Wanda yashiga gonata toh baya futowa a Raye. Tunda tashiga gonata toh taruga data tona kabarinta, kuma bayan nagama da itah zan gama da sauran na mallaki zoben datake jidashi. Dukiya tazama tawa ni the devilish mother. Hhhahahaha ta kwashe da dariya mugunta.

Zainab tace amma kada ki cutar min da Kabir kinsan shine rayuwata, mom tace kada kidamu da wannan babu abunda zan masa .kinajina idan kinje gida jigsaws mahaifin ki usman cewa dole ya hallarci taro yau domin akwai muhimmiyar abu dazan fada.

Zainab tace toh uwar shedanu, ni kinga mah nagaji da kayan likitocin nan Allah, Allah nake na je gida na ciresu, zainab tace yauwa Mom kada kimanta kishafa mata wannan laya abayan tah idan tasha maganin

Kuma please kada kimanta maganin bita zaizai dakuma na mallaka dakika ce zaki bani yau a taro

Mom tace Duk wannan bah matsala bace kedai kawai ki hada Kai dani mu kashesu domin na zama shugaba a qungiya, idan mukagama toh koh kaina kikace na sare miki zanbaki.

Zainab tace banda dai cire kaii, sai anjima sai mun hadu a qungiya, Dan Allah ki kulamin da kabir Dina. Okay mom tace, tareda lashe wayan.

Tsaki taja tareda fadin bakuga komai bah wlh yanzu aka fara wannan yakin . Sainasa zaman duniyar nan ta gagari kowanne daga gidan nan.

Juyawarta keda wuya taga Ummi,  fuskanta Duk shabe shabe da hawaye. Jikinta sai karkarwa yake,

Gaban Mom ne yafadi, inda tace kalisat yaushe kika shigo dakinan.
Tafada cikin faduwar gaba. Tafara nufan inda Ummi take,

Jada baya Ummi tafarayi tace kada... ki matso.. kusada.. Ni, tafada cikin sheshekar kuka.

Bantabah tunanin kina neman rayukan ahalin nan ruwa a jallo bah, Bantabah tunanin aka daga gareki bah.

Dama ke muguwa ce, Dama ke azzalumace Mara imani Mara tausayi, meye wannan ahalin suka rage ki dashi, mene kike bukata a duniyar nan da DAD baiyimiki bah.

Na tabbata soyayyar da yake miki batakai ta aunty amarya bah, amma aka kike so kikashe mana iyaye, sannan muma ki Gama da tamu rayuwar. Wace riba zakici kenen.

Me muka tare miki, meyasa saboda me, menene ribarki na aikata aka, tabbas ke macuciya ce, kuma tabbas ke kike cin naman mu batareda kin gasa bah.

Dafe kanta tayi Wanda yake mugun sarama mata tace, Meyasa, meyasa zai kasance kace zaki aikata aka,  tabbas da labari aka bani koh wuyana za'a kama a yanke bazan taba yarda bah, amma nagani dakaina,
Aba Mom ta karashe maganar hawaye na bin kuncinta.

Hatta  children da kika haifa baki Kyale bah wannan wace iriyar bakar zuciyace dake, tabbas idan aka ganki aka ga maciji toh afara kasheki kafun akashe macijin. Domin ke kinfi maciji illah.

Dan Allah koda zaki kashe kowa, meyasa zaki kashe amriya wane laifi ta aikata miki, yarinyarda babu ruwanta, meyasa zaki saka marainiyar Allah aciki,saboda mee, saboda mee.

Saboda itace ta Hana na kasheku tuntuni, zaro ido Ummi tayi tace kamar yaa kenen,

Kwarai mah kuwa, cewar mom, wannan yarinyar amriya ta taremun abubuwa da dama kujerarda za'a bani a qungiya tasaka aka fasa bani domin, ban cika alkawarin dana daukarwa qungiya bah.

Hatta kashe kabir da kwanakin baya dazanyi ita ta hana na kashe tah. Gashi yayi mugun tsananta amma Tana taimakarsa.

Kuma batareda yasan itace ta ceci rayuwarsa a teku bah, ita ta hanani kashe shi tun tuni, Domin shine farko a lissafi wadanda zankashe.

Tsuman tsaye Ummi tayi batareda ta iya furta wani kalmaba, tafara kukan bakinciki,

Tace Allah sarki amriya baiwar Allah dama ita ce yake tsaron rayukanmu agidanan takesa nata rayuwar a hadari. Wannan wace iriyar kyakyawar zuciyace da ita. Tabbas yahya Kabir baiyiwa amriya hadalci bah.

Tabbas wannan maganar bani kadaice zanji bah kowa na family saiya san Duk irin muganci dakike kullawa wannan family.

Direct hanyar waje tayi, shan gabanta Mom tayi Tareda sakin murmushin mugunta tace kina tunanin bayan kinsan sirrina zanbaki kifuta ne da ranki, toh imppossible.

Duk wanda yaruga daya San sirrina toh a ranar zai bakunci lahira, Dan aka,  idan kinje Chan lahirar kya basu labari achan.

Rike kan Ummi tayi Tareda bugawa akan bango.

Kara ummi tasaka tana kokarin cetan rayuwata amma ina akan yagaza. Daukan katon kwalba mom tayi Tareda rotsa wa Ummi akai, faduwa tayi jini yafara zuba akanta.

Fasa ihuuuu
Salma dake kofan dakin Tana video Duk abunda Mom tafada akan ahalin dakuma abunda tayiwa Ummi, wani ihuun yakara fasawa, wayan datake video dashi ya sabule yafadi.

Kallon kasa tayi tanemi wayan ta rasa. Jikinta ne tafara karkarwa,

Kallonta Mom tayi tasaki murmushin mugunta tace yata salma kenen,.

Kokarin guduwa Salma keyi. Amma kafun tayi wani yunkuri ta chafko Salman.

Ihuun taimako salma tafasa inda mom tasa hannu ta buga mata baki,

Cikin sheshekar kuka tace Dan Allah mom kada ki kashe Ummi, ni yarki ce ki kasheni tunda kekika kawoni duniya amma Ummi wacce bataji bah batagani bah, kuma sannan yarinya ce, na roke ki,  kirabuda itah ki kasheni please mom Tafada tana hada hannayenta guri daya, tareda fashewa da kuka.

Dariya Mom ta kwashe dashi tace ke yata ce bazan iya kasheki bah amma kuma idan takama don burina yacika babu Wanda bazan iya kashewa bah hatta kedinnan.

Amma for now bazan kasheki bah domin ke yata ce amma Ummi wannan confirm ne saina gamada rayuwarta.

Kuka salma takara fashewa dashi tace aba Mom Duk menene wannan Dan Allah ki kasheni ki rabuda ita, itama kamar yar ki fah take.

Allah ya kiyaye, wannan bah zata taba zama kamar yata bah, kinga kina batamin lck, kibarni na aiwatar da abunda zan aikata akanta.  Daukan wuka tayi tanufi inda Ummi ke yashe cikin jini.

Durkushewa salma tayi Tareda rike kafar Mom tafara kuka Tana bata hakuri, amma koh kallo bata isheta bah, saima tureta datayi tafadi kanta yabuge bango.

Hawayene yafarabin gefen fuskan Ummi, cikin matsanci ciwo da radadi tace, mom na roke ki, na yarda ki kasheni amma Dan Allah kibari naga mahaifiyata, inason namata kallon karshe, inason na mata sallama kafun na mutu. Yanda ruhi na zaifi kwanciya.

Na rokeki dan Allah da manzonsa, kibari Nayi wa mahaifiyata Kallon karshe, nice mafi soyuwa agareta, idan kika kasheni batareda tayimin Kallon karshe bah nasan zata iya rasa rayuwanta,

Na rokeki, takarashe maganar hawaye nabin fuskanta, mom bata yi wata wata bah ta tsinka mata mari, tace wato na kyaleki kije kitonamin asiri bah impossible.

Daga wukan mom tayi zata soka mata.

Ummi tace tabbas karshenki bazaiyi kyau bah, tabbas zaki haduda fushin Allah,

Kin kashe rayuka bah adadi, sannan nima yanzu zaki kasheni, bkm ki kasheni bissmillah , rintse idanuwanta Ummi tayi Tareda yin Kalman sha'ada, hawaye na bin kuncinta.

Batareda guntun imani bah Mom ta chaka mata wukan, Kara ummi tasaki, daga nan kuma numfashinta ya tsarke, alamun babu numfashin tattareda ita.

Innalilahi wa innahilahi rajihun.

Ihuun Salma tasaki, Tareda yinkan Mom a fusace, shake mata wuya mom tayi tace indai har burina zai cika banki na kashe kowabah. Buga kan Salma tayi ajikin bango, hatake salma tafadi sumammiya.
Wajan wardrobe dinta tanufa, Tareda jan wardrobe din gefe, Hatake wani kofan ya baiyyana,

Maganganu naji tafarayi wanda nima bansan metace bah, ba'afi mintuna biyu bah kofan ya bude, tanufi inda gawan Ummi yake tajata Tareda jefata cikin wannan kofan,

Takuma daukan Salma tasakata aciki.
Hatake kofan yarufe kansa.

Azabure amriya ta tashi tareda kwallah uban ihuu dayasa gabadaya gidan ya amsa, sosai su nadira dake kusada itah suka tsorata. Tashi tayi Tareda nufa hanyar waje.

Shan gabanta kabir yayi yace ke ina zakije, menene aka, cikin zafin rai da baccin rai tace, ka matsa,

Kabir yace bazan matsaba dukana zakiyi, kallonshi tayi da brown eyes dinta Wanda suka Kara rinewa sukayi brown ta daka mai tsawa, Tareda tureshi a hassale,

Sosai hankalin kowa yatashi.

Mom kam jin karan amriya tayi uwa saukar aradu bah shiri tafara goge jini dake akasa. Tareda feshe ko ina da turare.

Ganin hanyar dakin Mom zataje ,yasa kabir janyo hannunta. Tareda rungumeta.

Ba shirt tafara kokarin cire jikinta daga nashi amma ta gaza,  aka tacigaba da kokarin cire jikinta daga nashi amma tagaza, fashewa tayi da kuka, tana mai fadin ta kashesu wannnan azzalumar ta kashesu,

Aunty amarya tace wa aka kashe, sakinta Kabir yayi, suka ga tanufi dakin mom, babu bata lck suka bi bayanta,

Banka kofar amriya tayi, bah shiri Mom ta tashi, Tareda fadin yata amriya Lfy,

Kallon ta amriya tayi tace, menene suka aikata miki zaki kashesu, meyasa, sbd mee, meyasa zuciyarki tagama bushewa babu digon imani acikinta.

Kallonsu mom tayi ta fasheda kukan munafurci, tace yanzu ni amriya nice muguwa, mena miki,  Duk irin soyayyar danake nunamiki amma shine kike kokarin yimin sharri.

Amriya tace bah sharri zanyi miki bah, indai akane toh kibari na chaje dakinan indai kinada gsk, rass gaban mom yafadi,

Fashewa takumayi da wani kukan tace yanzu kin mayarda ni makaryaciya kenen, Kabir kaji abunda matarka take fadamin koh, kanajinta kayi shiru, zuwa inda take yayi yace aba mom kada kidaga hankalinki nasan mah bazaki aikata aka bah, kinsan batada Lfy, shiyasa take magganganu.

Amriya tace Lfy yana kalau wannan azzalumar matar Tana neman rayuwanka ruwa a jallo, Tass, tass ya sharara mata mari.

Tareda nunata da Dan yatsa tace, kada ki kuskure kishiga tsanina da mahaifiyata, wato sokike ki hadamu koh, ke wace iriyar mahaukaciya ce.

Mahaifiyata zakiyiwa sharri toh ta Allah bata ki bah banza shashasha, Mara hankali

Dafe kuncinta tayi wanda hawaye suka Fara zarya akai, Tareda girgiza kanta,

Tafuce daga dakin, suma su Nadira suka rufa mata baya. sosai ran kowannensu baiji dadin marinda Kabir yayiwa amriya bah.

Kiyi hkr mom kinsan yarinyar sai a hankali kamar mai tabin kwakwalwa.  Bkm kabir ainasani, Bb komi kaje kaci abinci kaji my son, OK mom, kuma kada ka manta ka rarrasheta.

Allah ya kiyaye Kabir yafada, murmushin mugunta mom tayi cikin ranta kuwa tace yanzu kaine nagaba a lissafina a Wanda zankashe.

Jin wayarsa yayi Tana ringing, sallama yayi wa mom Tareda fucewa daga dakin, ganin bakuwar number akan yasa yaki daukan waya, saida aka Kira wajan 10 miss call, ganin wanda ke kira bazai daina bah, ya dau wayan a fusace yace hello waye, waye yake addaban rayuwata da Kira.

Daga Dayan bangaren akace shin ina magana ne da Sir Kabir,  kabir yace Eh nine ya akayi.

Dayan bangaren akace toh kazo kudauki gawar yar uwarka Ummi yana bakin titi, gabadaya police da likotoci dakuma yan jarida Sun zagaye wajan.

What Kabir yafada tareda mikewa tsaye yace gawar Ummi Kuma.

Jin aka yasa gabadayansu mikewa tsaye, gaban kowannensu yafadi.

□□□□□□□□□□□□□□□□

TOH FAN'S MUJE DAI ZUWA

COMMENT & SHARE PLEASE □□□□□□

ALKALAMIN □□□□□□□□□□?
BABY ISHA □□□□□□
2/28/24, 22:12 - AISHA M.B (Baby isha): Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/JYYV16dbYaX1dykLX7EE91

□□□□□□□□□□□□□□□□□
□□□□□□□□□€□□□□□□€□□□□□□€□□□□□□€□□□□□€□□□?
□□□□□□

□□ BISSMILLAHI RAHAMANI RAHIM □□
ALJANAR RUWA CE □□□□□□□□□□? PAGE 3 □□□ 8 □□□□□□ 3 □□□ 9 □□□

WRITTEN & DIRECTED □□□ BY BABY ISHA □□□□

---
fucewa amriya tayi tanufi dayan dakin,

Kabir jiyayi kamar ya hadiye zuciya ya mutu tsabar bakin ciki, yau karo na farko a rayuwarsa da wata ta Kalli kwayar idonsa tagayamai mgn .

Mamaki yashigayi yana mai fadin ni Kabir mace tagayamin mgn kuma Nayi shiru how is that possible.  Tsaki taja Tareda fadin zatasan ta tabo kabir wlh.

Kwanciya yayi akan gado saiyaji gabadaya gadon mah babu dadin kwanciya, Tsaki yaja yatashi Tareda fucewa daga dakin yanufi, dakin da amirya tashiga.

Tura kofan yayi yace toh mai guri yazo mai taburma ya nadi.

Koh Kallon inda yake batayi bah saima kara gyara kwanciyanta datayi,

Gani tayi banza dashi akan yakara hassala shi yace ke bada ke nake bah koh bakiji bah, zoki fucemin daga daki,

Cikeda bakin ciki amirya ta tashi tace wai kai wane irin Dan takura ne, kace nabar maka wancan dakin nabaro Chan nadawo nan kai meyasa kawai burinka ka ga ka batamin rai. Aba Dan Allah wannan shirmen naka ya isheni, nagaji

Nabar maka wancan dakin na dawo nan kuma ka Kara biyoni yanzu kuma kanacemin wai in futa, toh wlh bazan futa bah.

Kabir yace nikike cewa bazaki futabah, shiru tamai ta koma kan gadon ta kwanta,

Shiru yayi yana mai hayyana irin rashin mutuncin dazai yiwa amriya, Chan gefen gadon yanufa, tareda daukan pillow sannan ya kwanta . Jan bargon yayi Tareda rufawa ajikinsa.

Ganin ya debe bargon gabadaya yasata, Jan bargon ta dunkuleshi ajikinta, ganinta kwashe bargo yasa shi kara Jan bargo. Aka suka dunga ja, amriya naja shima naja.

Daga karshe yasamu ya tureta tafadi akasa, tashi tayi, cikin jin aushi ta janye bargon gabadaya ta hada dashi kabir din, luuuu kabir yatafi sai ajikin amriya,

Faduwa sukayi, numfashi kowanne aicinsu na gogan najuna, rass gaban kowannensu yafadi, kabir kamm jin jikinshi yayi wani iri, sosai suke kallon juna bako kifta ido. Kamshi turaren amriya ne kabir yasaka Hatake yaji wani irin sanyi da shauki nashigarsa, a hankali yadunga lumshe ido, sosai kamshin turarenta ya burgesa.

Gyaran murya amirya tayi sai a lckn kabir yadawo hayyacinshi

Tashi kabir yayi yakoma kan gado sannan yayi aduar bacci ya kwanta, itama amirya aka ta tashi tanufi kan kujerar dake daki sannan ta kwanta akai. Bah shiri baccin barawo yayi hawan gaba da ita.

Juyawa kabir yayi yana fuskantar inda  take, Kallonta yayi, yaga yadda gashin kanta ya sauko. Murmushi yayi sannan yajuya ya kwanta.

Washe gari da sassafe amriya ta tashi inda tadora abinci na breakfast , bayan ta gama ta hajiye akan dining, sannan ta zuba wasu a kuloli Wanda zata kaiwa su DAD dake asibity.

Futowa kabir yayi cikin kananun kaya, kayan Ba karamin kyau suka masa bah, kallonshi amirya tayi, cikin ranta tace bah laifi kyakyawa nee amma sai iya shegen jaraba.

Harde hannuwanta amriya tayi tace ina kwana, koh Kallon inda take beyiba, ya nufi dining ,

Zama yayi sannan yabude kulan wani kamshi ne ya daki hancin shi, ya mutse fuska kabir yayi yace menene wannan, amriya tabashi amsa dacewa mee idonka ya ganar maka,

Murmushin takaici yayi tareda janyosa ya Kama bakinta ya murda, kara amriya tasaki, saida yaga ta jigata sannan yasaki leben.

Kara rinewa lebenta yayi  tace mugu kawai,
Kallon soya da Kwan data kawo mishi yayi yace wannan Ai shashanci nee , ina kika taba ganin anci abinci mai nauyi da sassafe,

Amriya tace bantaba gani bah toh akanka za'a Fara,

Kabir yace ni bazan ci wannan Abunba, murmushi amirya tayi tareda daukan kulan tarufeshi tasaka acikin basket tace abu yazo gidan sauki, yunwan CE bakaji dakanajin yunwan da ko tuwo nakawo maka zakaci.

Ni yanzu inaso zan kai wa su mami abinci Dan aka inason ka kaini asibity, Kallon bakida hankali kabir yamata yace,

Gsk yane wuyanki ya isa yanka, ni zakice nakaiki hospital Dan tsabar kin Raina min hankali,  kuma kin rainani.

Amriya tace toh in baka kaini bah wazai kaini, Dan Allah kayi sauri kada mu makara, kabir yace bazan jee bah, idan kinso kitashi sama,

Hawaye ne yafara ciko mata a ido tace, yanzu ace mami Tana asibity DAD yana asibity ga aunty amarya da gradma, na tabbata tunjiya babu abunda suka saka abaki sbd jimamin mutuwan Ummi, abincin dazasu saka fah aikinsu zan Kai musu,

Yanzu Dan Allah ... Bata karasaba taji yace shikenen, shikenen, ya isa banason takura, shirya mutafi.

Cikeda farin ciki amirya tace, Ngd, kabir yace karki dauka sbd kince nakaiki zankaiki, zankaiki nee sbd mahaifina dakuma mami suna Chan,.

Ya mutse fuska amriya tayi cikin ranta kuwa tace shidai wannan bazai taba chanzawa bah.

Tashi yayi Tareda daukan car key, yanufi hanyar waje ganin akan yasata bin bayansa .

Daidai suma su nadira na futowa daga part dinsu, gaggaisawa sukayi, inda suma sukadau mota, body guard suka bude gate din gidan suka fuce saura su amriya, Wanda yazage sai jamata aji yakeyi .

Mom ce Tafuto daga part dinta idanuwanta sun kada sunyi jajir Duk Sun kumbura tsabar kuka.

Ganin aka yasa hankalin kabir tashi da sauri yanufi inda mom take yace, mom what happened, meyafaru kinsan banason na ganki cikin Damuwa please mom kifadamin menene.

Share hawayenta mom tayi tace kabir, meyasa mutane suka fiye zalinci, yanzu ace yarinya karama kamar Ummi asamu wani mara imani ya kasheta,

Na rokeka kabir tabbas kasaka agano Wanda yayi kisan nan sannan agano Wanda yasace min yarinya Tana kaiwanan ta fashe da kukan muna furci.

Rungumeta kabir yayi, yace insha Allah mom zansa agano ko waye yanzu aka yan sanda suna bincike akan case dinsu Ummi nee insha Allah kuma za'ayi nasaran gano kowaye.

Murmushin mugunta mom tayi tareda Kallon inda amriya take ta kesta mata ido daya, ran amriya ne yakai kololuwar bacci, cikin baccin rai tace, Dan Allah kazo mutafi kada mubarsu, sunajin yunwa basuci komai bah.

Sakin mom kabir yayi yace mom bara muje mudawo zamuje asibity. mom tace toh nima mutafi tare zanje.

Cikin fusata amriya tace Aa mukadai zamuje, babu inda zaki bimu.

Kabir yace me kike nufi, amirya tace aba kalb yanzu so kake muje ta dunga mana kuka , baka ga yadda fuskanta ya kumbura bah, baikamata muje da ita, bah sbd kada taje ta dunga kuka, itama mami tafara kuka,

Kaga gwanda ta zauna a gida zuwanta babu abunda zai tsanana mana, zuwa inda mom take amriya tayi tace,

Mom kije ki huta kisha magani ki kwanta sbd baikamata ace kina ganin abunda zai daga miki hankali sbd halinda kike ciki.

Kabir yace mom amriya tafadi gsk kije ki huta, zamuje mudawo da gawar a mata sutura akaita gidanta na gsk.

Fashewa da kuka mom tayi tace za'a kai Ummi gidanta na gsk shine baza a barni naga gawar yata bah, sbd mee,

Cikin jin haushi da kunan rai amriya ta daka mata tsawa, Tareda fadin bayan kinkasheta, wato baki gamsu ta mutu bah shine kikeso kibimu, idan bata mutu bah ki karasata achan tantiriya, azzaluma, mai bushashiyar zuciya.

MANAGE PAGE PLS □□

COMMENT & SHARE □□□□□□
ALKALAMIN □□□□□□□□□
BABY ISHA □□□□□□
2/28/24, 22:12 - AISHA M.B (Baby isha): Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/JYYV16dbYaX1dykLX7EE91

□□ WRITER ASSOCIATION @@@@@@@@@@@@□□

□□□□□□□□□□□□□□□□□
□□□□□□□□□□□□□□□□□
□□□□□□□□□□□□□

BISMILLAHI RAHAMANI RAHIM □□□□

ALJANAR RUWA CE □□□□□□□□□□? PAGE 3 □□□ 9 □□□□□□ 4 □□□ 0 □□□

WRITTEN & DIRECTED □□□ BY BABY ISHA □□□□(AISHA M.B)

---

Firgit mom ta tashi daga mafarkin da takeyi, gabanta ne yafadi tace, yakamata Nayi wani abu kada yarinyar nan ta tona Min asiri.

Tashi tayi tareda daukan mayafinta tanufi hanyar waje a daddafe Dan dukan da amriya tayi mata bah kadan bane.

Futowa tayi harabar gidan, Daidai lckn taga su amriya suna kokarin Shiga mota.

Kabir tafada da Dan karfi, juyowa kabir yayi yace, mom ina wuni , mom ta amsa da Lfy son, ina zakuje aka.

Kabeer yace wlh zamu kai wa su mami abinci nee, Tom kabeer muje koh nima inason naje natayata jaje,

Kabir yace Aa mom kizauna ki huta koh.
Mom tace hutun me zan Zaune yi, yata amriya kice masa Dan Allah yabarni naje.

Amriya tace mom keda Danki ni ina ruwana, dakin ne fah, kinga kinada Dama kimasa Mgn yaji.

Kabir ya harari amriya, sannan yace shikenen mom Tunda kince aka muje, bude mata kofan motan yayi, tashiga,

Inda amriya tatsaya tazuba ido koh zai bude mata itama.

Ganin bata Shiga motan bah yasa yace ke bazaki shigo bah ne koh mee, kinafah batamin lck, amriya tace toh ni bazaka bude min kofan bah,

Binta yayi da kallo yace, Mace daya tilo takk zan iya budewa kofa a duniyar nan, itace mahaifiyata, so idan kinga bazaki iya budewa bah toh, wa kanki, musaimu tafi,

Ya mutse fuska amriya tayi ta bude kofan motan tashiga, masu gadi ne suka wangale musu kofa suka fuce.

Tunda sukafara tafiya Ba wanda ya kulla Dan uwansa saima sake sake ds kowannensu yakeyi.

Direct hospital din suka nufa, ba'afi 20minutes bah suka isa wajan, parking yayi yafuto daga cikin motan sannan yabudewa mom kofa ta futo daga cikin motan.

Sanin cewar bazai bude mata kofa bah yasa itama ta futo daga cikin motan, tareda futowa da food flask din, direct cikin reception din suka Shiga.

Tarar dasu sukayi a zazzaune kowa yayi tagumi, gaishesu su kabir sukayi, su aunty amarya suka amsa batareda walwalah a fuskokin suba.

Amriya tace Yauwa ga abinci na dafa muku, barana siyo Ruwa, Gradma tace munkoshi wlh,

Hade rai amriya tayi tace wlh Baku isa bah, sai kunci, murmushi DAD yayi yace Tom shikenen, daukan daya daga cikin flask din amriya tayi tace barana kaiwa mami nata abinci nasan tanajin yunwa.

Dad yace mushiga tare, tunjiya rabona naga yar uwata. Tashi sukayi gabadaya sukashiga cikin room dinda mami take. Da sallama sukashiga, inda mami ta amsa kasa kasa.

Murmushi amriya tayi tace mami ga abinci nakawo miki, kici kinji, idanuwan mami ne ya cika da hawaye tace Aa amriya nakoshi, kibarni da tarun bakinciki, da kuncin da nake ciki.

Amriya tace aba mami, Dan Allah kidaina fadan aka, Allah yarabamu da bakinciki, Allah kada yakawo abunda bazai wuce bah., abunda yafaru yaruga daya yafaru, Allah yaruga daya kaddara cewar Ummi zata mutu batareda kinyi ido hudu da itah bah, ki share hawayenki mami , mu fauwala wa Allah komai,

Bai kamata ace kina kuka bah aduar ki take bukata bah kuka bah,

Mami tace yanzu shikenen Ummi ta rasu, batareda ansan wanda yakasheta bah, yanzu auta tah ta tafi kenen.

Amriya tace aba mami kin manta kinadani, na miki alkawari zan Maye gurbin Ummi acikin zuciyarki,

Kuma Allah yatona asirin wanda yayi wannan kisan nan bada dadewa bah, munafukai masu idon jemage, Tafada Tana Kallon mom takeyi fari da ido.

Mami tace Dan Allah inason naga gawar yata, DAD yace bazai yuhuba sbd anruga da ankaita gidanta na gsk.

Wasu hawayen ne suka Fara zubowa, Mom tace Allah sarki Ummi Allah yajikan ki da rahama, yamiki rahama yasa aljanna firdaus ce makomarki .

Gabadaya suka amsa da Amin

Maryam wato mami cewar mom sannan tace Dan Allah kici abinci kinji,abunda yafaru yaruga daya faru zaizai Allah ya kiyaye gaba.

nadira tace, mami please, taya hankalin mu zai kwanta idan muka ganki a wannan halin.

Share hawayenta mami tayi tace shikenen Naji zanci , Yauwa mami naa, yanzu baranaje na siyo ruwa, wanda zaku sha,

Khalid yace kibarshi nizanje, Amriya tace Aa kana min bakinciki zanje Aiken mami naa, bakasan nasamu lada koh

, murmushi gabadayansu sukayi ,Tana kaiwanan tafuce daga dakin. Murmushi Kabir yayi karo na farko da amriya ta burge shi.

Kallon kabir mami tayi tace kabir gsk kayi dacen mata, kariketa hannu bibbiyu, karike matarka kuzauna Lfy, yadda hakkinta bazai aukanka bah itama hakkinka bazai aukan ta bah kaji, wlh sa'ar mata, irin Mace kamar amriya, mai tausayi da amana dakuma taimako daidaiku nee, kaji koh, kabir yace insha Allah mami Ngd, kifara cin abincin kafun takawo ruwan. Barana je nadawo yana kaiwanan yafuce,

futan shi keda wuya suka ci karo da abbansu Khalid, gaisheshi kabir yayi,  abba su Khalid Ya amsa .

Tareda fadin suna ciki kuwa, kabir yabashi amsa da cewar Eh suna ciki, OK tom shikenen Ngd. Kabir yace ya hkr, abba yace wlh Lfy Ngd.

Shiga dakin yayi da sallama a Bakinsa, inda su DAD suka amsa gaggaisawa sukayi, inda su DAD suka fuce suka basu guri.

Inda ake sayarda ruwa amriya tanufa inda mutanen wajan sai binta suke da kallo.

Sallama amriya tayi, inda mutanen wajan suka amsa,

Sannan tace abani ruwa na roba, mikamata mai ruwan yayi ta karba,  Tana shirin budewa tasha taji Ihuun mutane suna fadin aka mota ,aka mota.

Juyawarda zatayi taji anfado mata ajiki, daka tawa amriya tayi ta dago da matar. Daga jikinta bayan amriya matar ta tsaya sannan matar tafara mgn cikin dashashiyar muryanta tace, kada kibari su kama ni Dan Allah nidin bah mahaukaciya bace.

Daya daga cikin likitocin yace, ke yarinya ki matsa daga wajan matar nan mahaukaciya cee, tanada cutar mantau .tsintar ta akayi acikin ruwa . Yanzu sacatery za'a kaita shine take guduwa.

Kallon idanuwan matar amriya tayi tace Wacece kee, hada idanuwa sukayi da matar Hatake hankalinta yatashi, tarike hannuwan amriya sannan tace kece, kece, tabbass kece.

Kokarin cire hannunta amriya tayi tace ni Kuma menayi, matar tace ke zaki kawo karshenta, ke zaki gamadasu, dole ki gama dasu babu inda zalinci ya Dore, dole hasan cewar jaruma ta baiyyana, kada kibarsu, kada kirabudasu, ki yakesu har sai inda karfinki yakare yata.

Kada kataba gazawa, yakamata ace asan cewar kin baiyyana, mai kawo karshen zalinci ta zo.  Kitashi tsaye, kitada makamai ki yake su,

Taruke kafadar amriya tace kada kirabudasu na rokeki, ki kawo karshensu, tabbas zun debo ruwan dafa kansu, ki kashesu karki Kyale kowa. Tana kaiwanan matar tafadi summamiya , daukar matar sukayi suka feceda itah daga asibity.

sosai hankalin amriya yatashi ,jikinta yafara karkarwa. Karasowa kabir yayi ganin mutane sun taru aka yasa yaja hannun amriya suka bar wajan.

Bangaren su mami kuwa, Shiga ciki abba yayi yace sannu maryam ya jiki, sama sama, mami ta amsa.

Ajiyan zuciya abban su Khalid yayi yace, nasan nayimiki babban laifi, na tauye miki hakkinki a matsayinki na matata.  Bansan dawane ido zan kalleki bah, tabbas na aikata kuskure kuma nagano kuskurena, Dan Allah na rokeki kiyafemin ki gafartamin,

Na miki alkawarin cewa akan bazata sake maimaita kansa bah, Dan jimm mami tayi tace naji nayafe maka, Dan Allah kafuta zan kwanta.

Aba maryam kenen haryanzu fushi kike dani, ki taimaka ki yafemin, wlh bada San raina nake aikata, abunda nake yamiki bah, koh kishiyarki mah tuntuni na Dade da sakinta, kawai namiki karyar cewar ta tafi wajan iyayenta Hutu nee.

Mami tace toh ni ina ruwana da ita Ai bah akaina take zaune bah. Kowa zamansa yakeyi.

Murmushi dad yayi yace, matata kenen,  shikenen zan tsuguna Kuma na hada hannayena na rokeki Dan kisan da gsk nake
.

Kokarin tsugunawa yake, mami tayi Saurin mikewa tace Aa, ka rufamin asiri, sokake Allah yayi fushi dani, na yafe maka, toh idan mah ban yafe maka bah mezanyi, abunda yafaru yaruga daya faru, wlh na yafe maka duniya da lahira kuma.

Nice mah yakamata ace na nemi gafarar ka sbd magganganu dana fada maka Mara dadi, Dan Allah ka yafemin.

Abba yace aini babu abunda kukamin Kuma baki min laifin komai bah, akasari mah dalilin magganganu da kika fadamin yasa na gano kuskure naa, Dan aka na yafe miki. Murmushi mami tayi tace Alhmd ina mai godiya  a gareka, abba yace nine yakamata na gode miki.

Jijigata Kabir yashigayi Ganin tafara futa a hayyacinta,yasa yanufi gida da itah batareda yanar dasu DAD bah, direct daki yakaita, Tareda zaunan da ita

yace ke meyasa meki, meyafaru, Rike hannunsa tayi wanda zoben tah ke sanye tayi, tareda saita Daidai saitin zuciyarta ta dora, zoben akai, wani irin nutsuwa ne yafara ziyartatta,

dauke hannunsa zaiyi ,yaji takara kankame hannun tace, kada kacire hannunta katsaya, tsyawa yayi yana Kallon ikon Allah, rintse idanuwanta tayi sukacigaba da Tsayuwa wajan harta samu nutsuwa.

Dagowa tayi tareda sakin hannunshi tace kayi hkr na Rike maka zobe batareda izininka bah, ka yafemin, Kallonta Kabir yayi yace, meyasa wancan matar naga tarike ki, meyasa kike yawan faduwa idan kinga abu ko Kuma idan an watsa miki RUWA. Meyake faruwa dake kifadamin gsk, yau inason kifuto ki gayamin asalin Wacece kee, meyasa Duk wannan, fadamin Wacece kee.

Dago idanuwanta tayi wanda hawaye sukara zarya akan fuskanta, tace ni be kowa bace bace mutum irinka.

Yes I know, amma inason insan dalilin dayasa kike faduwa just like that, koh ki tsuma, kokuma akasarin aka, waye yayi sanadiyan faruwan akan.

Share hawayen dake bin kuncinta tayi tace, KAINE SILA . .....

□□□

(J.W.A)
Rubutu baiwa ce daga Allah, jajirtattu ne kawai kan iya amfani da wannan  asaitacciyar baiwa su sauya tunanin al'umma cikin sau i.

---
Jin furucinta yayi kamar saukar aradu. Juyowa yayi ya  da Kallon mamaki ya kalleta, ya ce "Kamar ya kenen? Ban fahimta ba."

'Dan jim Amriya tayi ta ce "Kwarai kuwa, kaine silan komai da yake faruwa da ni."

Kabir ya ce "Ni Kuma taya na zama sila? fad'amin ina jinki." ya karashe maganar fuskanshi a had'e.

Kallonshi tayi ta ce "Eh kaine, kuma har yau har gobe zan cigaba dafad'in kaine."

Kabir ya ce "Nifa ba abunda na tambaye ki kenen bah, tambaya ta itace tayaya ni nazama sila?" Ya fad'a tare da sunkuyar da kansa gefe.

"Amriya ta ce, ta yarda na ceci rayuwarka daga teku, wanda shine ta saka haryanzu ka kasance a Raye.."

A firgice ya juyo ya kalleta, da sauri ya mike idan ran kabir yakai dubu to ya 'baci ,ya ce "Harke kinkai kimin karya, wato kin samu labarin cewar wata ta ceci rayuwata, Kuma na kamu da sonta, wato saboda kinsan rauni na shine kike son kibi ta salon yaudara ki yaudareni, that can never be possible."

'Dago idanuwanta amriya tayi wanda suka kada sukayi jajir, ta ce "Dan Allah ka yarda dani , wlh ni ce na taimakeka, zobena ne a hannunka wanda ya su'buce ya fad'a hannunka, dan Allah ka bani zoben na koma duniyata, inba haka bah mutuwa zanyi na rokeka."

"Ya isa, wannan magganganu naki sun isheni haka, bana son na karajin komai daga bakin kii, sbd kin rainamin hankali shine zakice wai kece, toh duk wanda ya turo ki wajena domin ki zo ki yaudareni toh ki koma wajansa kice inji ni na ce hakan bazata taba faruwa bah impossible."

"Dan Allah ka saurareni, ka saurari abunda zancemaka, a halin yanzu ma rayuwarka dana Hosanna tana cikin hatsari, dan Allah kabani zobena domin na ceci wannan ahalin."

Kabir ya ce "A matsayinki nawa kenen? Ke wace? da zaki iya hana abunda zai faru, Kuma insha Allah babu wani abu dazai samu family nan, insha Allah duk wanda yake da mugun nufi akan wannan ahalin Allah ka mayar masa da niyarsa. wanda ba shine alkhairi bah agaremu.
Ke a matsayinki nawa zaki ce zaki taimake mu?"

Amriya ta ce," A matsayina na ALJANAR RUWA."  Kallonta ya yi da sauritare da yi mata Kallon up and down, ya saki dariya saida yayi mai isarsa sannan yace "Ke ALJANAR RUWA, wow, Kuma kinaso na yarda dake."

"Hmmm toh bara kiji wlh, kada mah ki fara fad'an haka sbd nidin nan babu abunda nafi tsana a duniyar nan sama da amin magana aljanar ruwa, banaso, dan haka maza kafucemin daga d'aki."

Tashi Amriya tayi tana shirin nufan inda yake, dakatarda ita yayi da fa □ in "Kada ki kuskure wallahi, maza leave my room or else, I will show you my true colour.."

"Me yasa ba zaka yarda dani bane?" Ta k'arashe magana tare da fashewa da kuka.

Jin ana bubbuga k'ofa yasa tayi Saurin share hawayenta, tareda nufa hanyar d'akin, ta murda handle din k'ofa, tare da bud'ewa, fatima ce tsaye hannunta rike da flask ta ce "Gashi inji Mom ta ce na kawo muku, na rana ne, Kuma na sanar miki cewar su Mami sun koma Lagos."

"Toh" Amriya ta ce, Kallonta fatima tayi tace, "Amriya lafiya kuwa naga kamar kinyi kuka meyafaru?"

Kabir dake cikin d'aki ya tashi tare da nufa hanyar waje inda ya bangaje amriya ya wuce.

'Daga ta fatima ta yi ta ce, "Sannu Amriya, menene aka yake faruwa ki fad'amin, yau Kuma wane laifi kika masa?"  fashewa Amriya ta yi da matsancin kuka ta ce "Allah sarki babu komi wlh."

Fatima ta ce "Toh amma me yasa kuke samun sa'bani kinga wlh Tunda su Docyor Amina da Aunty Amarya suka zo suka yi mana nasiha tun lckn nakeyi wa yaya Khalid biyayya. Kuma yanzu na koyawa kaina sonsa."

"Toh yanzu damai zamuji ga mutuwar Ummi, ga batar Salma da haryanzu jami'ai nemanta suke amma ace  mutum bazai fauwala Allah komai bah? Ki k'ok'arta ki Rike mijinki hannu bibbiyu."

Kallonta Amriya ta yi tace "Tom insha Allah zan k'ok'arta, fatima dan Allah kinada abun rubutu.?"

Fatima ta ce "Eh ina dashi me zakiyi?"Amriya ta ce, "Abu zan rubuta ne, ki aramun." Kallon kan table Fatima tayi ta ce "Yauwa ga wani bairo nan mah kinga saiki rubuta duk abunda kikeso."

Wajan table din Fatima ta nufa tare da d'aukan bairo din ta mikawa Amriya, kar □ a aAmirya tayi tare da yi mata godiya.

Daga bisani fatima ta fuce daga d'akin. Hajiye flask din abincin Amriya tayi, tareda goge Hawayen dake shirin zubo mata akan kuncinta.

Daki ta shige koh takan abincin bata bi bah, ta d'auki littafi, tafara rubutu.

Sai wajan karfe Tara 9:0 clock na dare Kabir ya shigo, tarar da ita yayi a Zaune tayi tagumi, tana ganin shi ta mike tare da fad'in "Sannu da zuwa, abinci ka yana kan dining." Koh takanta baibi bah, yanufi toilet tare da yin wanka ya futo yafara shafamai inda suman jikinshi suka kwanta sukayi luff gwanin sha'awa . Bayan yagama shafa mai ya mike tsaye tareda nufa kan gado zai kwanta.

Da sauri tace masa baka ci abinci bah fah, dan Allah kaci abinci kafun ka kwanta na safe  mah baka ci bah yanzu bazaka ci bah."

Kallon ta yayi ya ce, "Ina ruwanki cikin ki konawa? me yasa wai ke kinfiye nacin jaraba, wannan mata aka auramin koh annoba?"
Banza kawai, kinga ki futo kifad'a idan saki kike bukata toh ko yanzu zan dambara miki shi, so please don't disturb my life.  Ni zuwanki gidanan mah ba abunda yayi sai jawowa mutum mafisa da bala'i , banza kawai mai farar kafa."

 Kukane yaci karfin Amriya, hawaye mai zafi suka fara bin kuncinta, ta ce n"Ni □in, ni ce mai farar kafa, nice masifa koh, Allah sarki, □an Adam butulu ne."

Bayan gwagwar maya da wahalar da nake sha a sanadiyan kawai domin na tseratar da rayuwarku, shine zaka cedani mai farar kafa, wannan wace iriyar rayuwa ce?" Dafa kanta ta yi wanda yake mugun saramata ta ce, "Tabbas na aikata kuskure, meyasa ban tsaya acikin ruwa bah ankashe ni? Meya futo dani ya Allah me yasa na ceci wannnan bawan Allah naka, meyasa banyi zamana bah?"

Da nasan zan kasance a raye ne dan kawai naga wannan bakar ranar, da nasani na tsaya an kasheni."

Kallonsa tayi tace "Ko dan ina zamane a gidanku yasa kake min irin wannan rashin mutuncin? kodan an aura min kai ba tareda nak'i bah, koh sbd Banida kowa nid'in marainiya ce yasa ka ke aibata ni kake zagina da zalunta tah yadda kakeso."

Sosai jikin kabir yayi sanyi inda yaji tausayinta yayi mugun kamashi, tashi yayi yanufi inda take a zaune yace "Kiyi ha□uri, kinji nasan na aikata kuskure Kuma hakan bazata sake maimaita kanta bah."

Rungumeta yayi a jikinshi, inda itama ta rungumeshi, kallonta Kabir yayi yace yanzu kin yafemin, girgiza masa kai tayi tace "Eh, amma inason ka yarda da... " Shiiiiii yayi mata nuni da yatsanta. "please dan Allah kada kayi min zance d'azu abar maganan. Muje mu kwanta kohh, Yauwa kintuna min  zamuje muyi alwala muyi sallah, yau ina son na sauke hakkin ki dake kaina. Koda yake mah ni na riga da nayi alwala sbd aka kije kiyi alwala."

Rasss gaban Amriya yafad'i, hanjjin cikinta suka kad'a, ta ce, Kamar ya?" Kesta mata ido daya yayi yace aikin gane abunda nake nufi ko saina futo na baiyyana kije dan Allah."

Mikewa Amriya tayi inda gabanta bai daina bugawa bah, shiga cikin toilet tayi, tace "Nashiga uku yanzu ya zanyi, so yake muyi mu amala na ma'aurata."

"Taya hakan zai yiwu a matsayina na ALJANAR RUWA, shikuma BIL adama, wannan bazaiyuba, dole ne nasan yadda zanyi na kawar masa da hankali."

Tap din ta kunna Tareda Dauro alwala, Tana gamawa Tafuto waje, Jikinta sanye da towel.

Kallonsa tayi taga ya sauya shiga, cikin jallabiya yana kan sallaya yana lazumi,  saka kaya tayi tareda daukan hijabinta, tace "Nagama ma."

Tashi Kabir yayi inda, ya tada musu sallah, bayan sun idar da sallah, yayi musu addu'a, inda ya Rike goshinta yamusu aduan saduwa da iyayi.

Shaketa tayi jikin bango, Hatake matar tafadi, inda Mom taja gashin kanta, Kara matar ta saki, yana mai fadin "Ki rabu dani, muguwa, mara imani,
Me kikeso namiki, kin rabani da farinciki na, kin raba ni da d'ana, kusan shekaru 37.
Kin azabtar dani son ranki kin kulle ni a wannan dakin wajan shekara da shekaru. toh meya ra ge, kawai ki kasheni na huta.."

Dariya Mom ta kwashe da shi tace "Ke a tunaninki, narabaki da d'anki ne sbd kawai ina sonsa, toh barakiji, babu abunda nafi tsana a duniyar nan sama dashi, kuma saina ga bayansa tukunan hankalina zai kwanta ,Kuma keda barin d'akin nan har abada."

"Wallahi Allah yafi karfinki, insha Allah d'ana bazai mutu ta hannunki bah, wlh saidai shi yayi ajalinki, uuma ki sani matar d'ana tafi karfinki, kedin kinayi duk abunan ne kawai sbd abun duniya da ya rufe miki ido."

Itakuma haryanzu tana zaune ne a gidanan domin ta taimaka mana, kuma ita zata futo dani daga wannan bakin dakin dakika ajiyeni."

Mikewa mom tayi tace, "Tom shikenen basai in tana raye bah tukun zata taimkeki." fucewa mom tayi, tabar matar a tsaye. Tsugunawa matar tayi tareda fashewa da kuka, tace "Allah ka kawomin agaji.

Kasa wannan matar Ta gane gsk, kasaka ta gane hanya mai kyau.."

Washe gari da sassafe Amriya tanufi part dinsu DAD domin ta je ta gaishesu kamar yadda aka saba.

Tana cikin tafiya tafarajin kukan mutum, Juyawa tayi bataga kowabah, idanuwanta ne suka sauka akan k'ofan daki,  Amriya tace "Wai Wacece wannan matar dake cikin wannan d'akin, kitchen tashiga tareda ebo abinci acikin plate, dakuma RUWA, tanufi dakin dashi.

Bud'e d'akin tayi yauma kamar, kwanaki dakin duhu nee, kuna futula tayi, ganin matan amriya tayi ta chunkushe waje daya.

Hajiye mata abinci Amriya tayi tace "Ga abinci kici nasan dacewa kinajin yunwa."
Mika mata abincin Amriya tayi, barar da abinci matar tayi tace,
"Bana bukata, ina bukatar yarona, dana kawai nake bukata."

Fashewa matar tayi da kuka tace "Inason naga dana koda Kallon karshene kafun na mutu."

Amirya tace Waye d'anki, fad'amin nikuma namiki alkawarin cewar zankawo miki shi
."

Matar tabawa amriya amsa da cewar mijinki Kabir shine d'ana na cikina."

Rass gaban Amriya ya bada, Amriya ta ce "Kenen Mom bah itace Mahaifiyar Kalb bah? hakan yana nufin cewa kece fatima wacce aunty amarya tafadamin cewa kinrasa d'anki daga bisani kika rasu?"

Matar tace, "warai kuwa ina raye ban mutuba, wannan azzalumar matan ita tadunga azabtar dani bah kakkautawa, ki taimaka kiceci rayuwar dana."

Amriya tace, "Tabbas yau innan, zan tona mata asiri kowa saiyasan abunda ta shuka."

Tashi Amriya tayi tare da fucewa daga akin tanufi dakin Mom , tarar da mom tayi a Zaune tana shan lemon kwalba, Kallonta Amriya tayi tace "Tabbas kin tabbatar min da cewa ke din makura ce a fannin zalinci.."

"Dama bake kika haifi Kalb bah, menene wannan ahalin suka aikata miki da har suka cancanci irin wannan mummunan sakayyar."

"Kin kashe Ummi wacce bataji bah,  bata ganiba, kin batarda Salma wacce take ya ta cikinki, Ba iyasuba kinkashe mutane da Dama wanda bazasu irgu bah."

"Me yasa toh ki dakata aka, ya isa,  yau zan tona miki asiri kowa yasani agidannan."murmushi mom tayi tace, "Nizaki tonawa asiri? to na fiki hatsabibanci, kafun ke kitona min asiri nizan fara tona naki."

'Daukan wukan dake kan table mom tayi ta yanki Jikinta dashi, tareda fasawa kanta kwalba, inda ta jefawa amriya wukan."

Fa□uwa mom tayi kasa tareda fasa ihuu wanda yan gidan sukayo hanyar dakin.

Duk abunda Mom keyi Duk a idon Salma, amma babu halin futowa tafada sbd tana a kulle ne.

Bude kofa Kabir yayi, inda su nadira mah suka Iso gurin, Mamakine yakama kowannensu Ganin wuka a hannun amriya, ga mom rai a hannun Allah.

Direct wajan Mom kabir yanufa a firgice yace Mom meyafaru, Mom tace" Zata kasheni, ku taimakeni, kada kubari takasheni..
"

Kallon Amirya Kabir yayi, gaban Amriya ne ya fadi ganin idanuwansa sun kada sunyi jajir, tunda take bata taba ganin ranshi ya 'baci bah sai yau. Hatake yaji wani tsanan Amriya takara karuwa acikin zuciyarshi.

Tashi yayi tareda shake mata wuya yace , "Menene mahaifiyata ta miki kikeson kikashe ta dama ashe mashekiya aka auramin bansanibah?"

Kakari Amriya tafari , sakinta Kabir yayii , inda Amriya ta fara tari, idanuwanta suka ciciko da hawaye tace "Wallahi karya takemin sharri tayimin so take ace ni mashekiya ce."

Mom tace, "Kabir wlh bah karya nayi mata bah, Kuma abunda baka sanibah shine itace ta kashe Ummi sannan ta batar da Ummi sbd bataso na tona mata asiri yasata kokarin kasheni."

Zaro idanuwa gaba d'ayaba suka yi.

□□□□□□□□□□□□□□
Allah sarki amriya baiwar Allah koya zata kaya a nan gaba, mujedai zuwa. daga taku baby isha wato Aisha m.B.

COMMENT & SHARE PLS □□□□□□

ALKALAMIN □□□□□□□□□□?
BABY ISHA □□□□□□(AISHA M.B)
2/28/24, 22:12 - AISHA M.B (Baby isha): Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/JYYV16dbYaX1dykLX7EE91

ALJANAR RUWA CE □□□□□□□□□□? PAGE 4 □□□ 2 □□□□□□ 4 □□□ 3 □□□

WRITTEN & DIRECTED □□□ BY BABY ISHA □□□□□□ (AISHA M.B)

https://www.facebook.com/61556643936657/posts/122103978398221464/?substory_index=1596987511055341&mibextid=rS40aB7S9Ucbxw6v
*JAJIRTATTU WRITER'S ASSOCIATION*□□□
(J.W.A)
Rubutu baiwa ce daga Allah, jajirtattu ne kawai kan iya amfani da wannan □ asaitacciyar baiwa su sauya tunanin al'umma cikin sau □ i.□□□

---
Tass Amirya taji saukan mari a fuskanta, Dafe kuncinta tayi wanda ke mata zugi da radadi,

Kallon kabir tayi ta ce
"Meyasa zaka mare ni?
Saboda kawai na tsaya akan gaskiya, na tsaya, tsayin daka, domin cetan wannan Ahalin."

Shiruuuu, Nadira tafada da karfi, tareda fadin,
"Banyi tsanmmanin aka daga gareki bah Amriya, tabbas kin cutar damu, wane laifi muka Aikata miki? Shin mun taba cutar dake ne tun sanda kike Zaune a gidan nan, koh kuma mun taba tauye miki hakkinki, menene bamu miki bah, duda cewar bamusan ke Wacece bah, aka muka dauke ki kamar yar uwar mu, muka had'a kai muka zauna tare, amma kirasa da abunda zaki saka mana sai tsiya"

Kabir yace Toh a yau bah gobe bah zaki bar wannan gidan.

Dakatar dashi Aunty Amarya Tayi, tace Bai kamata ace kun yanke hukunci ba tareda, kunyi bincike bah, ku yanzu a Sanin ku da Amriya" ta taba yinkurin cutarda daya daga cikin wannan Ahalin? Dan Allah ku dunga bincike kafun yanke hukunci.

Share hawayen da ke shirin zubo mata tayi, tace naji na Amince cewar zantafi, amma Kuma dole a yau bah gobe bah, zan tona asirin wannan makirar" matar, Kallon Kabir Amriya tayi tace, wannan matar da kake Kira mahaifiya, kake bauta mata bah dare bah rana, toh itadin bah mahaifiyar kah bace bah, itadin basaja kawai takeyi, tana nuna cewar ita ta haifeka.

Fashewa" Mom tayi da kuka" tace,  yau ni ake karya tawa agaban yayana, da mijina, Allah saiya saka min, Tunda ni na Haifi abuna bah wani bah.

Nuna mata hanyar futa yayi yace, futa daga nan, banason na kara sake hada ido dake, na tsaneki, tsana mafi muni, bantaba tsanan wata Mace a duniyar nan sama dake.

Ka mata Ai ace nasa aka ma min ke, Jami'ai su tafidake, amma bazan yi Akan bah saboda ni nasan darajar Mace, Dan aka fucemin daga gida,

Amriya tace Dan Allah ku saurareni, zanyi maka bayani, wannan bah itace mahaifiyar kah bah, mom itace ta kashe Ummi, takuma batarda Salma.

Rike hannunta yayi yanufi hanyar waje da itah, kokarin kwace kanta takeyi, amma Ya cutura,

Tsakiyan parlour ya nufa Tareda jefata akasa, faduwa Amriya tayi, inda kafanta ya gurde, wani azzababben" Kara tasaki,

Maza kifuta daga gidanan, yafada tareda, jefa mata pillow" a fuska. Yana mai fadin' wai waye ya turoki? Me kike bukata daga wannan family? Shin kudine koh, Dukiya, kokuma" turoki akayi ki kashe wannan Ahalin.

Tukunan mah Wacece?
Mikewa Amriya tayi daga kasan da take, ta Kalli Kabir" tace, nidin ALJANAR RUWA CE,  daga teku na futo, Kuma nazo gidanan ne badan komai bah, Dan na karbi zobena da ta subuce tafada hannunka,  na ceci rayuwarka batareda nasan ko waye kai bah,

Bantaba tunanin da abunda zaka sakamin ba kenen,

Rike kanshi Kabir yayi yace ALJANAR RUWA, Aljanar ruwa,  kin isheni da wannan zance naki, kina tunanin, ni Kabir zan  yarda da zancenki cewar ke ALJANAR RUWA CE. Toh ki tsaya kiji ni da kyau, wlh babu abunda nafi tsana da kyama a duniyar nan samada ALJANAR RUWA, su suka hallakar da kakana, bazan taba manta da wannan mumunan ranar bah,

dalilin aka yasa, naci alwashin cewa dole saina zama mai company kifi,  don kawai nasamu aka mamun wadanda suka kashe kakana, Hmmm babu Wanda yasan asalin labarin, Dan aka, maza kifuta daga gidanan, Kokuma nasa a kulle min kee a magarkama.

Hada hannuwanta waje guda, Amriya tayi tace, "Naji basai ka yarda dani bah, amma Dan Allah ku yarda da maganata, da macuciya kuke rayuwa, wannan matar muguwa Ce, ita takashe Ummi, Dan Allah ku yarda dani. Gaskiya nake fada muku, ku taimaka ku ceci baiwar Allah dake dakin ....." Bata karasaba, taji Khalid yana Fadin tunda yace "kije, kitafi mana."

Mom dake bayansu tasaki murmushin mugunta, Tareda daukan ruwan dake cikin Glass Cup na kan dining table, ta watsa ma Amriya Ajiki.

Gurnani Amriya tafarayi, inda fatarta yafara sabulewa, faduwa kasa tayi, tana birgima, sosai tsoro da fargaba yakama ko wannensu,

A hankali, sufarta yafara chanzawa, har sufarta na ALJANAR RUWA ya bayyana.

Zaro ido gabadayansu, sukayi, kara su Khalid suka saki, inda gradma tafadi a wajan sumammiya.

Dafe kansa Kabir yayi wanda yakeji kamar, Hana buga masa guduma. Sadiq da Khalid da sauran yan dakin suka jaa da baya, banda Kabir dayayi zololo, yana Kallon tah.

Juyo da jelanta, na Aljanar ruwa tayi tace, "kwarai nidin ALJANAR RUWA CE, nafada maku cewar, nidin ALJANAR RUWA CE, amma kuka karyatani, toh yau na bayyana kaina"

Dama nace Duk ranar da akasan ni ALJANAR RUWA CE, toh zamana a gidan nan yakare. "A yaud'inan zan koma duniyata, banki bah kona mutu konayi rai."

Zan tafi, bazan sake dawowa bah, Hawaye ne, yafara bin kuncinta, share hawayenta tayi, da bayan hannunta, tacigaba da fadin, kiyafemin, Nayi muku karyar cewar, na manta abunda yafaru, kudin mutanen kwarai nee kun zauna dani,

batareda kunsan asalin Wacece ni bah, Kuma yau zaku rabudani, Dan kunsan asalin Wacece nii, ina godiya da irin kulawa da soyayya da kuka nuna min,
Allah yasaka muku da mafifi cin alkhairy.

Ni zantafi, zan koma inda nafuto, amma Kuma taya akan zata yiwu kenen batareda zobena bah, saidai na zauna, a duniyar ku, har sai sanda aka gindaya min cewar zan mutu, idan ban koma duniyata bah.

Kallon kabir tayi tace, nagode da irin wannan sakayyar. Kuma zaka dawo neman gafarata a gareka. Tana kaiwanan, halittar ta yadawo na mutane. Tashi tayi tanufi hanyar waje.

Dakata, taji Kabir yafada, juyowa tayi tace, meyafaru, Kabir yace kin manta baki karbi takardar sakin ki bah, kije na sakeki, saki daya.

Murmushi wanda yafi kuka ciwo Amriya tayi, tace, nagode sosai. Tana kaiwanan ta fuce daga gidan.
Sosai tausayin Amriya yakama su Aunty Amarya.

Direct wajan gradma da mom suka nufa Tareda .watsawa gradma RUWA, Hatake gradma ta farfado daga suman datayi, ririke kabir Tayi tace waiyyo, ku taimakeni, kabir yace aita ruga data yi tafiyarta,

Rike mom DAD yayi yanufi dakin shi da itah, domin yayi mata maganin ciwon dake kanta.

Tafiya Amriya keyi tana kuka, batareda tasan ko ina bah na layin,

Wani bishiya ta hango, akan yasa ta nufi inda bishiyar take tareda, zama a karkashin bishiyar,

Zama tayi, ta chunkushe waje guda, tana kuka, sheshekar kukan tane ya tashi wata mahaukaciya, dake kwance a wajan,

Tashi mahaukaciyar nan tayi, tanufi inda take,

Mahaukaciyar ta ce, "Kai wanene wannan, me yasa kike kuka."
Tausayin Amriya ne yakama wannan, mahaukaciyar, daga Amriya mahaukaciyar tayi, hada ido sukayi da mahaukaciyar, da sauri mahaukaciyar taja da baya. Tana fadin kece, kece,

"Tabbas kece, Kallonta Amriya tayi, tabbas ta gane wannan matar, itace na jiya wanda ta gani a asibity."

Cikeda tausayawa, Amriya tace,
"Kedin Wacece, waye ya mayarda ke aka, menene kika aikata, ke dama asali mahaukaciya ce?"

Tsugunawa mahaukaciyar tayi, tareda fashewa da kuka, tace,

"Dama ni mahaukaciya ce, bansaniba, Dama hauka nakeyi, shikenen Ashe Dama ni mahaukaciya ce, Dama Banida lafiya."

Rike hannunwanta, Amriya tayi tace, ki nutsu, kada kidamu zaki, zaki samu lafiya da yardar Allah.

"Zan warkar dake, zaki daina hauka, Kuma Duk wanda, tayi miki aka saita dandani kudarta."

Rike hannun matan Amirya tayi gamm, Tare da rintse idanuwanta, Hatake aka Fara wani iska, Tareda guguwa, wanda ya gauraye gabadaya ilahirin, wajan.

.

MANAGE PAGE PLS □□□□

COMMENT & SHARE □□
ALKALAMIN □□□□□□□□□□?
AISHA M.B (Baby isha)

2/28/24, 22:12 - AISHA M.B (Baby isha): https://www.facebook.com/61556643936657/posts/122103978398221464/?substory_index=1596987511055341&mibextid=rS40aB7S9Ucbxw6v

JAJIRTATTAU WRITER'S ASSOCIATION □□□?
(J.A.W)
Rubutu baiwa ce daga Allah,jajirtattu ne kawai kan iya amfani da wannan kasaitacciyar baiwa su sauya tunanin al'umma cikin sauk'i □□□

ALJANAR RUWA CE □□□□□□□□□□? PAGE 4 □□□ 3 □□□□□□ 4 □□□ 4 □□□.

WRITTEN & DIRECTED □□□? BY BABY ISHA □□□□ (AISHA M.B)

---
Jikin mahaukaciyar ne ya fara karkar wa, ta fara shure shure da kafafunta, lokaci daya matar ta kwallah kara wanda ya gauraye dajin.

Daga bisani Kuma tayi Tsit alamun ta tsuma. Kallon ta Amriya tayi, cike da tausaya wa, tace insha Allah zaki samu lafiya, babu wanda zai Kara Kiran ki mahaukaciya,

Tana gama fadin aka ta Mike tsaye Tareda jin ginar da matar a jikin bishiya, daga bisani Kuma tayi tafiyar ta.

Saida dare yayi sosai
matar ta farka daga baccin da takeyi, Kallon Jikinta tayi, taga gany'an yak'i da datti a jikin tah.

Salati tasa ka tana mai fadin, meya ke faruwa dani, menene wannan Kuma? Taya akayi nazo wajan nan. Tambayar data Shiga yi wa kanta kenen. Rike kanta tayi domin ta tuna sanadi yar tah fada wa cikin wannan yana yin, amma akan ya cutura. Ba yadda ta iya, aka tafara ciccire dattin dake jikin ta.

Kallon ko ina na jejin tayi, tace yanzu ta ina ne zan gane hanyar gida, haske ta hango daga Chan nesa, akan yasa ta karasa wajan domin ta nemi taimako".

Zuwan ta keda wuya" ta tarar da Amriya a Zaune a wajan tayi tagumi. Kallon ta matar tayi cikin far gaba da tsoro tace! Sannu baiwar Allah.

Dagowa Amriya tayi ta dora idanuwan ta akan matan. Ganin aka yasa Amriya Mike wa, tace laa kinsamu lafiya, yanzu zaki iya fada min wanda yayi miki wannan aika-aikan

Cikin rashin fahimta doct khadija tace! Kamar ya kenen, Dama kin San ni ne,

Amriya tace, Eh nice na warkar dake daga ciwon hauka da kike, inaso ki fada min Wanda yayi miki aka.

Dafe kanta doct khadija tayi, sai a lokacin ta fara, tuna abunda ya wakana a baya. Kallon Amriya tayi tace,

Wata  azzaluma,Mara imani, wacce babu tsoron Allah koh ka d'an a zuciyar tah,Dan zuciyar tah a bushe take. Koh d'igon imani batadashi

Kallon ta Amriya tayi tace, koma Wacece wan nan baza ta taba kai mom rashin imani bah.

Doct khadija tace,wacece ke, meya kawo ki cikin jejin nan tsakar daren nan ,

Amriya tace wacce tayi sanadi yar ki fada wa wannan halin da kike ciki, toh nima itace ta kawo ni jejin nan, tayi amfani da makircin ta wajan kora ta daga gidan.  Na tabbata matar nan saita gasa musu haya a hannu,saboda bana nan, Kuma tasa ka sun koreni, Tana nuna musu soyayya a fili, ba tareda sun San cewar azzaluma ce bah.

Doct khadija tace kina nufin Karima devilish mother,  Amriya ta bata amsa da fadin kwarai  kwarai ita,

Doct khadija tace kenen ke wace a wajan su. Kallon doct khadija Amriya tayi tace, nidin matar wanda take karyar cewar danta ne,

Doct khadija tace kenen kema kin san  bah ita ta Haifi Kabir bah? Amriya ta bata amsa da cewar kwarai na sani.

Share hawayen da ke kokarin zubawa Amriya tayi, sannan tace kuma na daukar wa kaina alkawari cewa nida Kara dora kafana a wannan gidan har abada. Koda kuwa akan zaiyi silan ruguje war rayuwa ta, Dama lokaci kalilan ne ya rage mun a raye, kasan cewa ta Kuma ALJANAR RUWA, akan bazai sa na kara taimakon wannan ahalin bah.

Ajiyan zuciya doct khadija tayi tace, tabbas Dan Adam butulu ne, amma kada dalilin aka yasa ki k'i karasa ladar ki na taimakon wannan ahalin, da nice na samu damar da kika samu a wan nan gidan toh da tunan na tona asirin Karima, na bayyana gaskiyar da ke boye wajan shekara da shekaru. Amma ina akan bazai yuhu bah saboda, taruga ta hura musu wutan tsana ta a zuciyoyin su.

Dan Allah inaso ki koma gidan, ki karasa aikin ki, ke kika dace ace kin kammala wannan aikin bah wani bah, saboda kema ta sha feki.

Kwance yake akan makeken gadon sa, yana juyi.gabadaya ya kasa samun nutsuwan sa, tashi yayi, yafara Kai kawo a cikin dakin.

Zama yayi sannan ya dafa kansa yace, menene yake faruwa da ni ne, Meyasa na kasa samun nutsuwa tunda na Kori yarinyar nan. Kardai ta yimin asiri, back to sender, yafada yana shafa kansa.

Daukan wayar sa yayi, ya fara Kallon videos na shiek tijjani, aka ya ci gaba da kalla har aka zo kan wani video.

Playing yayi, yafara kalla, su Ummi ne da nadira wajan upstairs, suna cewa nadira taje, zata yi nasara, shikuma a lokacin sadiq ya kunno kai, Tana shirin fada wa kan kabir, tafada jikin Sadiq.

Dariya yasaki, yana mai fadin wai Dama aka nadira ta ke sona ban sani bah, Gashi Allah yaba ta, mafi alkhairy agare ta.

Next video ya kunna Tareda Kara volume, Amriya ce Zaune tana kuka inda su nadira sai rarrashin ta suke,

Amriya tace Dan Allah inason zanje na basa hakuri, kalisat tace ke haka zalunta Kuma kece da Bada hakuri,

Amriya tace kawai inason zan Bashi hakuri, dalili na mom ta wanka masa mari, da wane ido kike so ya kalle ni, wlh bana son naga abunda zai bata masa rai. Ta karasa maganar Tareda fashe wa da kuka.

Sosai yaji tausayin ta ya kama sa, shafa fuskan ta yayi,ta wayan yace, Allah sarki tabbas na sani cewa koda yaushe cikin kun Tata miki nake,

Baki taba roka ta wata alfarma na cika miki bah, tabbas nidin mugu ne Kuma mara imani, tabbas Nayi dana sani, kiyi hakuri ki yafe min.

Murmushi Aunty Amarya ta saki, babu Kalman da take furta wa sai Alhmadulillah, Alhmadulillah, abunda take ta Nana tawa kenen.
Share hawayenta Aunty Amarya tayi, san nan ta fara Kwan kwasa kofan dakin.

Saurin hajiye wajan yayi, yace, yes who's that at this late time. Aunty Amarya tace nice Kabir,

Kabir yace come in, Shiga ciki Aunty Amarya tayi, tare da samun guri, a gefen gado ta zauna.

Cikin rashin fahimta Amriya tace taya ta shafe ni, menene hadi na dasu, nima zobe na ne ya kai ni gidan, amma da babu abunda zaisa na futo duniyar mutane .asali mah ni na tsani Bil Adama saboda ya wanci su, basuda imani.

Dan aka babu abunda zai kara hada ni da wannan gidan, tunda na barta toh na barta kenen. Zobe na Kuma sai dai na mutu, amma nida gidan nan Ar abada.

Doct khadija tace, kada ki ce aka Amriya na sanki fiye da tunanin ki, a tunanin ki yau na fara Ganin ki, Aa na sanki shekara da shekaru.

Dan aka dole ki koma cikin wannan ahalin, saboda a nan zaki San asalin Wacece ke, menene sanadin fada warki wannan halin, taya ya kika zama wata jinsi da ban bana mutane bah, toh Duka tambayar ki, amsar ta itace wannan ahalin, sune zazu baki amsar tambayo yin ki.

Mikewa Amriya tayi a fusace tace, ni na ce inason Sanin wani abu game da rayuwa ta ne, bana bukata, domin ko na sani koh ban sani bah, lokaci kalilan ne ya rage min a duniya.

Kuma nidin ALJANAR RUWA CE, bah mutum bah, wato so kike na koma wannan ahalin da suka watsa min kasa a ido, akan baza ta taba faruwa bah, Dan aka idan zaki yi wani zance kiyi amma banda, koma wa tah cikin wannan ahalin.

Dan jimmm doct khadija tayi tace, nima a lokacin da, babu abunda ban fada bah, nace bazan kara koma wa wannan ahalin bah, amma nice yanzu nake rabar su, domin na ceto rayu kansu dake cikin hatsari.

Amirya tace wannan Kuma su ta shafa bani bah, tsakanin su ne wannan, su suka San laifin da suka yi har wannan matar take neman rayu kansu ruwa a jallo.

Doct khadija tace, ni kuma idan kika min wannan al farman, kika koma gidan, toh na miki alkawarin cewar,

Zan nuna miki mahaifiyar ki,  juyowa Amriya tayi da sauri, tace kin San mahaifiya ta ne, nifa mahaiya ta! ta mutu, Kuma ita din ALJANAR RUWA CE bah BIL adama bah,

Murmushi doct khadija tayi tace, kwata kwata, mahaifiyar ki bata mutu bah, Kuma ita din bah ALJANAR RUWA bace, mutun ce kamar kowa.

Amriya tace kenen  mahaiya ta, bah ALJANAR RUWA na ce, BIL adama ce, Kuma tana raye .

Toh Meyasa zata tafi ta barni wajan shekara da shekaru. Meyasa ta wulakan tar dani, bata ko ne mana, akan yana nufin kenen bata damu dani bah? Kokuwa akan yana nufin bata sona.

Doct khadija tace kada kiyi wa mahaifiyar ki gurguwar fahimta, asalima ita bata San kina raye bah, Kuma babu ranar da zata tashi ta fadi bata yi kuka akan ki bah.

Dan aka idan kika cika min alkawari wajan tona asirin Karima, toh tabbas zan kaiki wajan tah.

Share hawayen ta Amriya tayi tace, shikenen zan tafi, zan koma gidan badan komai bah Dan na cika miki muradin ki, amma daba Dan aka bah, da bazan Kara zuwa gidan bah.

Yauwa doct khadija tace, sa'anan ta ce shikenen yata Allah yadawo dake lafiya,

Mi kewa Amriya tayi, lokaci daya jiri ya di beta , da sauri doct khadija ta rike ta, Tareda zaunar da ita tace, meya faru,

Amriya tace wallahi ban sani bah ,tun dazu nake jin zuciya ta na tashi.

Kallon idanuwan Amriya doct khadija tayi tareda Kallon tafun hannunta, tace shin kin keda mijin ki, kun taba yin mu amala ta aure.

Cikin jin kunya, Amriya ta rufe fuskan ta da tafi hannun ta, tace, Eh sau daya ne.

Doct khadija tace kina cikin kunci, ga abun farin ciki ya riske ki,  toh na taya ki murna kinada juna biyu,

Zaro ido Amriya tayi gaban ta yayi mummunan faduwa, tace juna biyu fa kika ce, nidin Kuma,

Kallon ta doct khadija tayi tace, me ya faru, kamata ai ace kina farin ciki, da irin wannan abun.

Amriya tace, bawai bana farin ciki bah, tunanina daya ne shine nasan Kalb bazai taba son Dan da zai futo daga kar kashi na bah.
Saboda nidin ALJANAR RUWA CE, Kuma babu abunda yafi tsana a duniyar nan sama Da jinsi na wato na Aljanar ruwa. Kuma ni ina matukar sonsa.

Yanzu Gashi lokaci da ya rage min a duniya kalilan ne. Doct khadija tace kada Ki taba sare wa akan abunda kike so ,dole da jajurce warki da Kuma adua, shine zaisa ki cimma burin ki wanda yake kyakyawa.

Bai ka mata ace ki shiga gidan cikin bakin ciki bah, ka mata ai ace kishiga cikin farin ciki da annashuwa,

Yanzu ki kwantar da hankalin ki, kije gidan cikin karfin gwiwa, Kuma ki fada masa cewar ki nada juna biyu,

Nasan tabbas bazai k'i ki bah. Maza ki tafi, ki Kara karfafa wa kanki gwiwa kada ki saduda tun,kije ki fuskan ce shi, nasan tabbas zai fahimta.

Godiya amriya tayi wa doct khadija, cikin farin ciki ta bar wajan. Tareda nufa hanyar gidan su Kabir.

Aunty amarya lafiya na ganki acikin wannan lokacin,  murmushi Aunty Amarya tayi tace, kwarai kuwa lafiya,

Shawara nazo na baka, badan ko bana sonka bah, sai don soyayya da nake maka da Kuma, yan gidan nan.

Okay Tom ina jinki Aunty. Aunty Amarya tace , Kabir inason ka saura reni da kyau, inason fada maka abu dake cin rai na na wajan shekara da shekaru,

Kabir! Dago wa yayi ya kalle ta sannan yace na'am aunty, Aunty Amarya tace, ina son na fada maka cewar, Duk abunda Amriya ta fada dazu babu karya acikin ta, tabbas abunda ta fada gaskiya ne. Mom itace ta kashe Ummi Kuma....  Bata karasa bah taji yace,

Aba Aunty, aba Aunty, koda kowa zai biyi bayan aci dun duniyar mom ai bazaki ciba .

Na tabbatar miki da cewar karya Amriya tayi wa mom, so take ta hada mu nida mom dina, Kuma bata San Allah yafi karfin tah bah.

Murmushi Aunty Amarya tayi, sannan tace, Allah sarki Amriya baiwar Allah, kina taimako, kina sa rayuwar ki a hatsari amma basu San kina yi bah,

Kace ka tabbatar cewa karya Amriya take koh!  Kabir yace yes of course, am 100% sure that, karya take yiwa mom.

Aunty Amarya tace tunda ka tabbatar, toh menene hujjar kah.

Kabir yace ni Banida hujja amma nasan mom can never do such thing, idan mah tayi ribar mee zata ci, Amriya kawai yar leken asiri ce, maybe wani ne ya turo ta gidan nan.

Wai kai Kabir Meyasa baza ka yi nadamar abunda kakeyi bah?
Saboda mahaifiya ta, ta tsaya min, Kuma Duk mahaifiyar da ta iya tsaya wa domin Kare rayuwan danta, babu wata ma'alukiya da zata iya cin galaba akan tah.

Kenen kana nufin Amriya bah mutuniyar kirki bace,

Dai dai lokacinda Amriya ta karaso cikin gidan.  Jin muryar Kabir tayi, taji yace kwarai kuwa, Amriya bah mutuniyar kirki bace,

Chakk Amriya ta tsaya, Tareda jigina ajikin kofan Tana jin abunda yake fadin.

Kabir yace tunda yarinyar nan ta dora kafa fuwanta a gidan nan, toh tun lokacin masifa da baka'i suke ta faruwa, tabbas yarinyar nan bah mutuniyar arziki bace.

Da nafara dana sani abunda na aikata mata, amma shigowar ki yanzu, yasa na tuna da cewar tabbas mashekiya ce , muguwa Kuma, Mara imani. Baby macen da nafi tsana a duniyar nan sama Da itah. Na tsane ta, na tsane ta, tsana mafi muni, kinga Kare war Ta mah, bana son na kara hada ido hudu da ita, banason na Kara Ganin ta har abadan abada.

Hawaye ne suka Fara gangaro wa daga idanuwan Amriya,  hannunta ne suka Fara Kar kar wa, kuka ne ke shirin subuce mata Saurin rufe bakin ta tayi, Tareda rintse idanuwanta jin zuciyar take kamar zata futo..

Tashi tayi daga jikin dakin, inda kuka ya ci karfinta.

Juyawa gabadayan su sukayi, inda Kabir yace waye a nan.

Saurin rufe bakin ta tayi, Tareda Saurin barin  gidan.

bude kofan Kabir yayi yaga babu kowa, futowa Aunty Amarya tayi tace shikenen, ni zan wuce, ina fatan ka gane gaskiya. Tana kaiwa nan  tayi fucewar tah.

Ya mutse fuska kabir yayi tareda rufe kofan ya koma kan gado ya kwanta.

Tafiya Amriya ta farayi batare da tana cikin hayyacin ta bah.  Dafa kanta tayi wanda ke mugun Sara mata. Jiri ne yafara di banta, a daddafe ta karasa wajan junction. Tareda samun guri ta zauna.

Kallon kanta tayi, ta fashe da matsancin kuka mai cin rai.

Meyasa, Meyasa, wannan wace iri yar jarabbta ce, wannan wace iriyar bakar kaddara ce,  Meyasa na ka sance a raye har yanzu. Dama na kasan ce a raye ne don kawai naga wannan ranar bakin ciki, ranar da bata da gobe.

Meyasa tun tuni ban mutu bah, na tsane ka Kabir, na tsane ka,  bana son sake hada ido dakai, bana kaunar kah,

Kuma wannan ajiyar da ka bani, zan Adana tah har karshen rayuwa ta. Zan kula da abun ciki na har numfashi na, na karshe.

Tabbas zan Nisan ceka, kamar yadda ka bukata , bazaka sake haduwa da koh inuwa ta bah. Karuga da ka Gina min tsanan ka acikin zuciya ta. Rayuwa tah da komai nawa, nasa a hadari don kawai naga, baka cutu bah, amma akan baisa ka gani bah.

Ta karashe maganar tana mai fashewa da kuka, mai ratsa zuciya.

□□□□□□□□□□□□□□□□□
COMMENT & SHARE  PLS □□□□□□

ALKALAMIN □□□□□□□□□□?
BABY ISHA □□□□□□
(AISHA M.B)

2/28/24, 22:12 - AISHA M.B (Baby isha): https://www.facebook.com/61556643936657/posts/122103978398221464/?substory_index=1596987511055341&mibextid=rS40aB7S9Ucbxw6v

JAJIRTATTAU WRITER'S ASSOCIATION □□□?
(J.A.W)
Rubutu baiwa ce daga Allah,jajirtattu ne kawai kan iya amfani da wannan kasaitacciyar baiwa su sauya tunanin al'umma cikin sauk'i □□

ALJANAR RUWA CE PAGE 44?45

WRITTEN & DIRECTED BY BABY ISHA (AISHA M.B).

---

Kallon wajan gidan Amriya tayi tace, ya Allah, kada ka kawo abunda zaisa na Kara sanya kafafuwa na acikin wannan gidan, insha Allah baza ka Kara ganina bah na har abada, har abadan abada.

Mike wa tayi, ta Fara tafiya, Chan cikin dajin wajan ta nufa ta tarar da doct khadija a Zaune, Kallon ta doct "khadija tayi cikin rudewa tace,

yata Amriya, me yafaru?, Meyasa kike kuka? shin Kabir  ya Kara bata miki rai nee? tambayar da doct khadija ta Shiga yi wa Amriya kenen.

kuka Amriya ta Kara fashe wa dashin cikin, kuna da bakin ciki, tace doct khadija na aikata wani kuskure mara goguwa a rayuwa ta, wai shin yaushe kuka na da bakin ciki zai zo karshe,

Nayi dana sani futowa daga ruwa nazo duniyar mutane, Meyasa banyi za mana a ruwa bah, Kalb  ne yayi sanadin futowa ta daga ruwa , abunda na futo karba daban, abunda na tarar daban, Meyasa

na tsane shi, banason sa, tunda aka yake so zaiga asalin tsana Daga Aljanar ruwa, wallahi, yanzu ji nake kamar na kashe shi nima na kashe kaina.

Saurin rufe mata baki doct khadija tayi tace, Aa Amriya kada ki Bari zuciyar ki ta kaiki nesa, kada ki Bari shedan ya rin jaye ki, komai yayi farko zaiyi karshe, ma hakuri mawada ci, idan kikayi hakuri zaki dace.

Amriya tace, hakuri na me, hakuri na nawa, wane hakuri ne nan banyi bah a wannan rayuwa, ya wulakan ta ni, yaci min mutunci, zagi ba dare bah rana, yace min kaskantaciya, Duka zagi Ba bu abunda baiyi bah.

toh fadamin shin Nayi hakuri koh banyi bah, na tabbata da wata ce bani bah, wallahi saita iya kaishi ga hallaka..

kinga Dan aka yaje na bar masa zoben, Dama rayuwa tah bata da amfani, Kuma cikin kwanan na zan mutu, kamar yadda gumurzu ya fadamin.  inaso zanga abunda zan haifa a duniya kafun Allah ya dauki raina.

insha Allah babu abunda zai same ki cewar doct khadija, ta cigaba da fadin, kada kidamu, duda cewar Ahalin Muhammad sun tsane nii, saka makon sharrin da Karima ta min, amma akan bazai hana ni na je na bayyana musu gaskiya bah, dole Su san abunda Karima ta shuka.

Karima tayi min abubuwa da Dama Mara misaltuwa. ta raba ni da yan uwana, ta rabani da yar uwata mafi soyuwa a gareni, ta kashe min dana, Wanda iya shi Allah ubangiji ya bani, ta sanya na raba da da mahaifiyar sa, ta kuntata wa rayuwa ta.

tasa na aikata babban zunubi amma akan baisa ta rabu dani bah, dole ne na dauki mataki akan tah, shiru bazai yi magani bah, saidai abu ya Kara baci.

Amriya tace, Dan Allah inason kikaini wajan mahaifiyata, inason zan ganta.

Kallon ta doct khadija tayi tace, zan kaiki kamar yadda kika bukata amma yanzu lokacin kaiki baiyi bah, dole sai mun kashe wutar dake ci a gidan Muhammad kafun na kaiki,

Amriya tace bazan karya rantsuwa ta bah, nice miki bazan sake dora kafana akan wannan gidan bah.

murmushi doct khadija tayi tace, bazan ga laifin ki bah, saboda kina da hujja tayin akan, Kuma akan bazai sa naji bah dadi bah,

Amriya tace zan cigaba da zama na a nan dajin har sai lokacin da zan sauka lafiya. Aa Amriya" bai kama ta ki zauna a nan bah, kama ta Ai ace kin samu gida, Wanda za'a dunga kula dake.

ki tawo Tareda ni, zan kaiki gidan ka wata doct Amina, na tabbata zata kula dake harda abun cikin ki.

Aa doct khadija, ki barni na cigaba da zama a nan shine zai fiye min sauk'i, saboda idan ina cikin jama'a, zan dunga jin zuciya tah na kuna, inaso na zauna ni kadai.

Aa Amriya kiyi hakuri,  ki tawo dani muje, Banaso na kaiki gida na, saboda har yanzu Karima bata San ina Raye bah, Kuma idan ta gano baza ta bar ni har ke bah, Dan aka ki tawo na kaiki gidan kawa ta Dan Allah.

shikenen, zanje amma da sharadi, Doct khadija tace inaji ko menene ki fadamin .

Amriya tace, zaki je gidan su Kalb, kamar mahaukaciya, Kuma sannan kice musu, mahaiyar Kalb Tana Raye, what doct khadija tace, Tana mai fadin kinsan ko me zanyi bazasu taba yarda bah, Amriya tace kawai kiyi abunda na fada miki .

shikenen, Doct khadija ta fada, Tareda fadin, zanje Kuma zan fada musu. insha Allah gobe goben nan.

ki taso muje gidan doct Amina,cewar doct khadija.  Amriya tace, Aa ki Bari gobe. Tom shikenen, Allah ya kaimu goben.....

Washe gari da sassafe Amriya da doct khadija suka wuce gidan doct Amina.

Kwan kwasa gate din gidan sukayi, inda mai gadi ya bude musu Ganin doct khadija ce, yasa mai gadi ya bar su suka Shiga, yayi musu rakiya har wajan corridor din, parlour. Shiga ciki doct khadija tayi bakin ta rike da sallama.

Kabir inason muyi wata magana mai mahimman ci da Kai, dago kai Kabir yayi ya dora idanuwansa akan mom yace mom inajin ki.

mom ta cigaba da fadin,  kasan wannan yarinyar kirkin wato zainab yar gidan Alhj usman, Kabir yace Eh nasan zainab, naga yarinyar Tana da tarbiya, Kuma tana da hankali, mezai hana ka aure ta domin d'aga darajar Ahalin mu.

Dan jimmm, Kabir yayi, yace naji dadin wannan Shawarar mom, amma am sorry to say, i can't marry zainab, she's not my type.  bata Kai tsarar da zanso tah bah.

and mom as for me, inada wacce nake so, Kuma ni ban shirya yin wani aure bah yanzu gaskiya. Mom tace, shikenen Kabir, amma na Tambaye kah, shin tunda kake ka taba tambaya ta wani abu a duniyar nan, ban maka bah.

Duk abunda kake bukata shi nake maka amma, shine bazaka iya cika min wannan muradi nawa bah, shikenen bakomai, zaka iya taciya.

Dafe kansa kabir yayi yace, mom ki tambaye ni wani abu ko menene zanyi,.amma banda auren zainab.

mom tace, auren zainab shine muradina, inason ka aure ta, Dan Allah, ta Fada tana hada hannayen ta guri guda.

shikenen mom naji zan aure tah, cikeda farin cikin jin furucinsa, mom tace da gaske kake zaka aure ta. Kabir ya bata amsa da cewar da gaske nake zan aure tah, shikenen kinyi farin ciki koh, ya fada yana Murmushi, mom tace farin ciki mara misaltuwa mah.

yanzu inason yau kaje ka ganta a gidan su, kaji, Tom mom naji, farin cikin ki shine farin ciki na, banason na ga bacin ranki kwata kwata,

tashi yayi yace, zan tafi saina dawo, mom tace Allah ya dawo dakai lafiya. Kabir ya amsa da Ameen.

Kallon su Nadira Kalisat tayi, tace, kuna Ganin abunda aka yiwa Amriya yayi Daidai kuwa, Meyasa za'a yanke mata irin wannan tsatsauwar hukuncin.

Nadira tace, Meyasa ba za'a yanke mata bah, kokarin kashe mom fa tayi, Kuma ita ta kashe Ummi, kama ai  ace an yanke mata hukuncin kisa.

fatima tace kwarai kuwa, amma saboda yahya Kabir yaji tausayin ta yace tayi tafiyar ta, mu mun rike ta da hannu bibbiyu., bamu taba yin kurin kashe ta bah.

kalisat tace dukkan ku, bakuda tunani , a ranar da abun ya faru,. naga mom da idanuna ta dauki ruwan dake kan dinning ta watsa wa Amriya.

Nadira tace toh Dan Mom ta watsa mata ruwa mene akan yake nufi, kalisat tace mom ta Daidai tah lokacin da Amriya ta keson fadar wata magana.

kinga akan yana nufin Mom tana da wani kulla kulla acikin ranta, Kuma akan yana nufin Amriya bah karya ta fada bah, gaskiya ne,

Fatima tace Aba Kalisat, Meyasa bakida tunani nee, wannan abunda kike fada, babu hankalin da zai daukeshi, koda kin fada babu Wanda zai yarda saboda, Mom baza ta taba aikata abunda zai cutar da wannan Ahalin bah bare Kuma y'ay'an tah.

Kalisat tace hakane, amma saina war ware abunda ya sanya kowa cikin duhu.

Nadira tace oho Ke kika sani, kya yi kya gama, amma Duk abunda zaki yi, daga karshe Mom itace da gaskiya Ba Amriya bah.

mikewa Kalisat tayi tace, aida yar uwarku ce bazakuBazakuce aka bah, amma kuma ni ina goyon bayanta, zan tsaya mata har sai inda karfina ya Kare, zan nuna mata cewar Tana yar uwa kuma wacce kuma zata tsaya mata tsayin daka, domin futo da gaskiya. Tana kaiwanan tayi fuce warta.

ikon Allah doct khadija nake gani aka a gida na, murmushi doct khadija tayi tace, Eh wallahi, hayyuka ne suka min yawa shiyasa kika ga bana zuwa office.

doct Amina tace wa nake gani aka kamar Amriya, gaishe ta Amriya tayi, amsawa doct Amina tayi da fadin lafiya kalau y'ata, ya mijin naki, da fatan yana cikin koshin lafiya.

Sosa Kai doct khadija tayi tace yana lafiya, Tareda fadin Amina inason mudanyi wata magana dake a sirrince, doct Amina tace, okay bah Damuwa,

Kallon
Amriya doct khadija tayi tace Amriya ki shiga daki kinji, Tom Amriya ta tace tareda mikewa tsaye, ta nufi cikin guest room.

komai da komai, daya faru doct khadija ta zayyane wa doct Amina, amma doct khadija bata ce mata Amriya ALJANAR RUWA CE bah.

Girgiza Kai Doct Amina tayi tace, Dan Adam ba'a iya masa, babu komI kawa ta, zan kular miki da ita har Dan cikin ta, kada kidamu itama ai tamkar y'ata take.

godiya doct khadija tayi wa Doct Amina, doct Amina tace Aba kawa tah ai a tsakanin mu babu godiya.

tashi doct khadija tayi tace, shikenen ni zan tafi, inaso zan kai wa yan uwana ziyara,

shikenen toh Allah ya kaiki lafiya cewar doct Amina, amma shin bazaki tsaya kici breakfast bah, Aa wlh na koshi. saina dawo tana kaiwa nan doct khadija tayi fucewar tah.

bayan fucewar doct khadija, doct Amina taTaShiga dakin da Amirya ta Shiga, Amriya na ganin ta ta Mike, Aa y'ata zauna mana cewar doct Amina.

me kike so kici zan dafa miki, Girgiza kanta Amriya tayi tace na koshi, wannan Kuma bazai yuwu bah, babu abunda kika ci fah amma shine kike cewa kin koshi, toh ki taso akwai abinci akan dining kitawo muje muci koh, sannan na baki magunguna kisha.

Amriya tace Aa na koshi, banajin yunwa, doct Amina tace toh shikenen nima bazan ci abinci bah,kowa ya zauna aka.

murmushi Amriya tayi hawaye na son zubo mata Saurin share su tayi tace shikenen, Doct Amina muje zanci .murmushin jin dadi doct Amina tayi tace Yauwa y'ata ko ke fah,

taso muje koh, bayan mungama cin abinci zan ce da babban dana yusuf ya kaiki shopping kiyi siyayya ,shima kidauke shi tamkar yayan ki  kinji  .

tashi sukayi suka nufi dining, inda suka tarar Abban yusuf da yusuf na Zaune, da alama su suke jira.

serving dinsu doct Amina tayi ,inda itama taja gefe ta ibi nata, suka Fara ci.

oh my God sir Kabir ne yau a gidan mu, Kuma wai yazo hira wajena, Tsaki Kabir yaja, yayi murmushin takaici yace, ke ni yanzu zan tafi, idan na tafi ki kira Mom kice mata bakya sona bazaki iya aurena, bah inba aka ranki ya baci.

zainab tace Aba masoyi yaushe kazo, da har zaka tafi, shikenen zan fada mata amma Dan Allah inason ka kaini shopping, yau ranar fah masoya nee Valentine day, ya Kama ta ace ka bani babbar kyauta,

toh nida ke naga Ba soyayya muke, bah Dan aka, ki kiyaye ni kinsan ni bah tsarar ki bane wallahi,

aba sir Kabir please, and please, Dan Allah, ke naji shikenen, zan jiraki a waje, wlh idan baki futo bah nan da 20second, tafiya zanyi, Dan bazai yu nazama, bawan ki bah tohh.

yana kaiwa nan yayi fucewar shi , Kai na rawa Zainab ta dauki gyale Dan karami wanda dashi gwanda babu.

futowa tayi ta Tarar dashi yana shirin tafiya, Saurin daka tar dashi tayi sannan ta Shiga cikin motan, yabar harabar gidan.

Yauwa Yusuf inason ka kaimin kanwar ka shopping, kaji, yusuf yace Ammi consider it done. ni naga shirya wa, ban dai sani koh kanwa ta taga ma shirya wa bah.

Amriya tace ni a shirye nake, bayan sun gama cin abinci, yusuf ya dau mukullin mota yayi hanyar waje, hijabi, Ammi ta bawa Amriya, saka wa Amriya tayi ta bi bayan yusuf, bude mata gaban mota, Yusuf yayi ta Shiga.

tareda barin harabar gidan. direct shopping mall, suka nufa, Daidai lokacin suma su kabir na isa wajan.

bude wa Amriya kofa yusuf yayi , futowa Amriya tayi daga cikin motan suka nufi cikin mall din.

Rike hannun kabir zainab tayi wafce hannun sa kabir yayi yace ,are you normal, kada ki karamin irin wannan abun in badan Mom bah Allah koh a matsayin yar aiki bazan iya daukan ki bah bare Kuma azo kan wai mata.

hakuri zainab ta Bashi inda suka Shiga wajan mall din.

inda ake saida kyaututuka suka nufa, gabadaya masoya sun cika wajan, kowa yana siyawa budurwarsa kyauta.

saida su yusuf suka gama siyayya sa'an nan suka nufi wajan saida gift, Yusuf yace kan wata yau fah ranar masoya nee bazaki siya wa masoyinki kyauta bah, Amirya tace bani da masoyi. yusuf tace toh muje ni na siya miki saina baki kyauta a matsayinki na kanwata,

Aa wallahi ka barshi, nagode, Yusuf yace no bazan yarda bah, wato kina k'in kyauta daga wajan yayan ki.

wajan da ake saida Valentine Gift yusuf ya nufa da Amriya.

wata kyauta Kabir ya dauko ya damka wa zainab, Cikeda farin ciki zainab ta rungume shi,a bai nan nasi. Daidai lokacin idanuwan Amriya suka sauka akan su Kabir.

Cikeda bakin ciki da takaici, Amriya tajawo yusuf tace inason mubar nan wajan, Dan Allah, yusuf yace why? baki ga wasu masoya bah sun rungume juna, Dan aka kawai ki bari na siya miki.

Saurin cire jikinshi kabir yayi daga na zainab yace, ke wace mahaukaciyar ce, taya zaki rungume ni a gaban jama'a.

bakida hankali ne, kayi hakuri, kaji my love.

Cikeda takaici Amriya ta dauke idanuwan ta daga kansu, ta Kalli yusuf tace, sweetheart, ni wannan nakeso tayi nuni da hannun ta,.

da sauri kabir ya juyo jin kamar yasan wannan muryar, hada ido sukayi da Amriya Hatake gaban shi ya fadi.

Amriya ta cigaba da fadin Sweet, wannan nake soo, yusuf yace kada kida mu, zan siya miki koma Wanne,

wani irin kishi ne ya turnuke zuciyan Kabir, nufan inda suke yayi tareda Jan hannun Amriya yace, waya baka izinin futa da matar wani, kaidin waye

ke Kuma ya fada yana Kallon Amriya, Dama Ashe ke yar iska ce, uban waye ya baki izinin futa da wani na mijin, Dama abunda ke faruwa kenen idan ka auri karuwa,

Tasssss Amriya ta tsinka wa Kabir mari.

zaro idanu jama'a wajan sukayi. nuna Kabir Amriya tayi da Dan yatsan ta tace...
.

COMMENT & SHARE PLS

KUYI HKR JIYA KUNJI SHIRU WLH WAYANA NE YASAMU MATSALA,
AMMA INSHA ALLAHU ZAN GYARA

ALKALAMIN AISHA M.B ( BABY ISHA)

BISSMILLAHI RAHAMANI RAHEEM
ALJANAR RUWA CE PAGE 45&46
WRITTEN & DIRECTED BY
AISHA M.B (BABY ISHA)

---

Cikin baccin rai Amriya tace, har kai waye, Da zaka zo ka neman cimin zarafi agaban jama'a, shin na taba ganin ka ne ,koh kaidin mijina ne, da zaka zo kana ci min mutunci,

Bansan ka bah, baka Sanin bah, toh ina ruwan ka dani, kazo da masoyiyar ka, nima nazo da nawa, shin akwai laifi ne aciki, toh ka sani, aure ce ta hada ni dakai , Kuma yanzu ta raba, Dan aka baka da iko akaina, baka San irin muguwar tsanan da nayi maka bah, tsanan da nayi maka koh ma'auni, bazai iya aunawa bah, Kuma kayi na farko, kayi na karshe. Kada koda gigi yasa ka kara aikata min aka, Dan wallahi, bazaka jita da dadi bah.

Idanuwan "Kabir ne suka kada sukayi jajir! cikin zafin rai, yace ni kika mara, kin manta waye ni, Amriya tace taya zan iya manta da Kai, Dama ai mutum baya taba manta alhery da mutum ya masa, kai baka min alhery bah, aka sin aka mah, zalunta ta , kake yi,

Kallon shi tayi tace, tsaya wa ina magana da Kai bata lokaci ne,  maida Kallon ta kan yusuf tayi tace,  sweet,  Dan Allah ka tawo mu bar wajan nan, naga yan hassada da k'eta, sun cika nan wajan,

Zuwa daf, da wajan zainab tayi tace, ke me kike da suna, wallahi, Kabir yafi karfin ki, kada ki sake kiyi wasa da wuta, domin kuwa idan ta fusata, baza ki ji da dadi bah.

Kallon "Zainab Amriya tayi tace, ke daka ta nan , ni bah sa'ar wasar ki bace, kije kifara ji da matsalan dake damunki, kafun ki kara fada wa a wata matsalan, wallahi, Duk abunda na miki toh ke kika siya da kudin ki.

Tsintar kansa kabir da yin shiru, Amriya na kaiwa nan, ta bar wajan, bin bayanta yusuf yayi,

Tsaki Kabir yaja, ganin kallo gabadaya ya koma kansa, fucewa shima yayi daga wajan, inda zainab ta bi bayan sa, Tana Kiran sunan sa.

Shiga cikin mota yayi, ya tada motan sannan da mugun gudu ya bar harabar wajan, zainab na Iso wa taga yabar mall din.

Tunda suka Fara tafiya babu Wanda ya ceda wani cikan ka, yusuf ne yayi karfin halin fadin, Meyasa kika tozarta Kabir a bainan jama'a, Kuma Meyasa kika ce ni masoyin ki ne, bayan Kuma ni bah masoyin ki bane.

Aba Amriya, Shifa mijin ki ne, bai ka mata  ace kin masa irin wannan rashin mutunci bah, bai kamata mah ki mareshi bah, why Amriya, Why?

Dago fuskan ta tayi, wanda suka jiku da hawaye tace, Duk abunda Nayi masa shiya siya da kudinsa, ni menene bemin bah, zagi, Duka, babu abunda baiyi bah.

Tabbas bai kama ta ace na maresa, bah, amma meyasa zaice min karuwa?  Kalman da na tsani akira ni dashi, ba iya ni kadai bah,  koh wata macen da tasan daraja da kiman ta ta d'iya Mace , ba zata, so a kira ta  da Kalman karuwa bah,

Yana min Duk abunda ya gada ma, banta rama wa, bah, amma yau, yakai ni kololuwar makurar karshe,  shiyasa na maresa, Kuma nasan akan bai dace bah,

Cigaba da tuki yusuf yayi, Har suka isa gida,

END OF BOOK 1

COMMENT & SHARE
ALKALAMIN
A'ISHA M.B
(zinariyar jajirtattu)